# JIRWAYEN BA-XOKI DA XARSAU A LITTATTAFAN *JIKI MAGAYI* DA *IDON MATAMBAYI* DA *GANXOKI*

**DAGA**
**ABUYAZID ISHAQ YUSUF**
**SPS/15/MHA/00004**

**KUNDIN BINCIKE DA AKA GABATAR DOMIN CIKASA WATA QA'IDA TA NEMAN DIGIRI NA BIYU A FANNIN ADABIN HAUSA (M.A. HAUSA) A SASHEN KOYAR DA HARSUNAN NIJERIYA, JAMI'AR BAYERO, KANO.**

**OCTOBA, 2019**

**TABBATARWA**

Na tabbatar da cewa wannan bincike da na gabatar mai suna Jirwayen Ba-xoki da xarsau a Littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki* ni ne na rubuta shi da kaina, bisa jagorancin Dakta Ibrahim Garba Satatima, da Dakta Anas Sa'idu Muhammad. A iya sanina ba a gabatar da wannan bincike a wani wuri ba, kuma babu niyyar sake gabatar da shi a wani wurin don neman shaidar kammala wani karatu a nan gaba.

______________________________
ABUYAZID ISHAQ YUSUF
SPS/15/MHA/00004

## AMINCEWA

Wannan kundin bincike ya samu dubawa da tantancewa tare da amincewar waxannan manyan malamai.

________________________________

Farfesa Ibrahim Garba Satatima
Jagoran Aiki
(Supervisor)

________________________________

Dakta Anas Sa'idu Muhammad
Mai Duba Aiki na Gida
(Internal Supervisor)

________________________________

Farfesa Magaji Tsoho Yakawada
Mai Duba Aiki na Waje
(External Supervisor)

________________________________

Dakta Ibrahim Garba Satatima
Shugaban Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya
Jami'ar Bayero Kano.

## SADAUKARWA

Na sadaukar da wannan aiki ga mahaifiyata Hajiya Halima Alfanda, da mahaifina Alhaji Ishaq Yusuf da kakata wadda Allah ya amshi rayuwarta a cikin wannan shekara, wato Hajiya Hasana Abdullahi (Baba ta Gwauron Dutse). Haka kuma sadaukarwa ce ga Honourable Aminu Sulaiman Goro.

## QUNSHIYA

*Shafi*

*Tabbatarwa* : : : : : : : : *ii*
*Amincewa* : : : : : : : : *iii*
*Sadaukarwa* : : : : : : : : *iv*
*Qunshiya* : : : : : : : : *v*
*Godiya* : : : : : : : : *viii*
*Abstract* : : : : : : : : *xiii*
*Tsakure* : : : : : : : : *xiv*

**BABI NA XAYA**
**SHIMFIXA: : : : : : : : 1**
1.1 Gabatarwa : : : : : : : 1
1.2 Manufar Bincike : : : : : : 2
1.3 Dalilin Gudanar da Bincike : : : : : 3
1.4 Muradan Bincike : : : : : : 12
1.5 Tambayoyin Bincike : : : : : : 12
1.6 Farfajiyar Bincike : : : : : : 13
1.7 Ra'in Bincike : : : : : : 13
1.7.1 Dangantakar Ra'in da Binciken : : : : 17
1.8 Tarihin Marubutan Littafin *Jiki Magayi* : : : 18
1.8.1 Tarihin Marubucin Littafin *Idon Matambayi* : : 21
1.8.2 Tarihin Marubucin Littafin *Ganxoki* : : 22
1.9 Kevavvun Kalmomin Bincike : : : : 23
1.10 Naxewa : : : : : : : 25

**BABI NA BIYU**
**BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA : : : 26**
2.1 Gabatarwa : : : : : : : 26
2.2 Ayyukan Magabata : : : : : : 26
2.3 Naxewa : : : : : : : : 41

**BABI NA UKU**

**DABARUN GUDANAR DA BINCIKE**


3.0 Gabatarwa : : : : : : : 42

3.1 Sigar Bincike : : : : : : : 42

3.2 Matakan Gudanar da Bincike : : : : 43

3.3 Samfurin Bincike : : : : : : 44

3.4 Makamashin Bincike : : : : : : 46

3.5 Hanyoyin Tattara Bayanan Bincike : : : 46

3.6 Qalailaice Bayanan Bincike : : : : : 47

3.7 Xa'ar Gudanar da Bincike : : : : : 48

3.8 Kammalawa : : : : : : : 49


**BABI NA HUXU**

**JIRWAYEN DABARAR BA-XOKI DA XARSAU A LITTATTAFAN *JIKI MAGAYI* DA *IDON MATAMBAYI* DA *GANXOKI*: : : 50**


4.1 Gabatarwa : : : : : : : 50

4.2 Fayyace Nau'o'in Ba-xoki a Littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki* : : : : 50

4.3 Tarken Matanonin Ba-xoki a Littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambay*i da *Ganxoki* : : : : 51

4.3.1 Ba- xokin Gaske na Kusa : : : : : 51

4.3.2 Ba-xokin Gaske na Nesa : : : : : 63

4.3.3 Ba-xokin Gangan : : : : : : 74

4.4 Tarken Matanonin Xarsau a Littattafan *Jiki Magay*i da *Idon Matambay*i da *Ganxoki* : : : : 84

4.4.1 Xarsau na ban Tausayi : : : : : 85

4.4.2 Xarsau na ban Dariya : : : : : 95

4.4.3 Xarsau na ban Takaici : : : : : 98
4.4.4 Xarsau na ban Mamaki : : : : : 106
4.4.5 Xarsau na ban Tsoro : : : : 112
4.4.6 Xarsau na Farin ciki : : : : 115
4.4.7 Xarsau 'Yan Tagwai : : : : 117
4.4.8 Xarsau na Gangan/Zulaƙe: : : : : 123
4.4.9 Xarsau Jirwaye da Ba-Xoki : : : : 125
4.5 Naxewa : : : : : : : : 129

**BABI NA BIYAR**
**KAMMALAWA : : : : : : : 130**
5.1 Gabatarwa : : : : : : : 130
5.2 Gudunmawar Bincike : : : : : 130
5.3 Iyakancewar Bincike : : : : : : 132
5.4 Shawarwari : : : : : : : 132
5.5 Kammalawa : : : : : : 133

*Manazarta : : : : : : : : 135*
*Rataye : : : : : : : : 138*

# GODIYA

Godiya ta tabbata ga Allah maxaukakin Sarki, wanda ya ba ni iko da lafiya har na sami damar kammala wannan bincike. Salati da aminci ga shugaban farko da na qarshe, Annabi Muhammad, sallallahu alaihi wa sallam, da iyalansa da kuma sahabbansa.

Ina matuqar godiya ga iyayena, Alhaji Ishaq Yusuf da Hajiya Halima Alfanda.Ina roqon Allah ya yi musu sakamako da mafificiyar Aljanna, ya yi musu rahama kamar yadda suka raine ni a lokacin da nake xan qarami. Ina yi musu godiya da fatan Allah ya ja kwanansu.

Godiya mai yawa ga Dakta Ibrahim Garba Satatima, jagoran duba wannan aikin. Haqiqa ya taimaka mini qwarai ya ba ni dukkan agajin da na buqata ba tare da gajiyawa ba, musamman ta fuskar duba wannan aiki da kuma yin gyare-gyare haxe da shawarwari waxanda suka daxa haska mini hanya wajen gudanar da wannan aiki. Allah ya yi masa sakayya da maxaukakiyar Aljanna, ya ja kwanansa, ya raya masa zuriyya cikin tafarki madaidaici.

Ina godiya ga jagoran duba aiki na cikin gida, wato Dakta Anas Sa'idu Muhammad. Haqiqa ya ba ni dukkannin dama da lokacinsa wajen ganin samun nasarar kammaluwar wannan bincike,musamman

ta fuskar duba wannan aiki da kuma yin gyare-gyare, haxe da shawarwari waxanda suka daxa haska mini hanya. Haqiqa babu abin da zan ce da shi sai addu'ar Allah ya yi masa sakayya da Aljanna ya kuma qara xaukaka shi, amin.

Haka zalika, ina miqa godiya ga jagoran duba wannan aiki daga waje, wato Farfesa Magaji Tsoho Yakawada. Haqiqa ya yi matuqar qoqari wajen daxa gyara wannan bincike ta hanyar yin gyare-gyare. Allah ya yi masa sakayya da aljanna.

Har ila yau, ina godiya ga malamaina na Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya na Jami'ar Bayero Kano, waxanda suka haxa da: Farfesa Abdulqadir Xangambo da Farfesa Sa'idu Muhammad Gusau da Farfesa Isa Mukhtar da Farfesa Ahmadu Bello da Farfesa Yakubu Magaji Azare da Farfesa Aliyu Musa da Farfesa Aliyu Mu'azu da kuma Farfesa Usman Usaini Fagge.Har wa yau dai, ina godiya ga sauran malamaina da suka haxa da: Dakta Murtala Garba Yakasai da Dakta Halima Abdulqadir Xangambo da Dakta Muhammad Tahar Adamu (Baba Impossible) da Dakta Ahmad Magaji da Dakta Aminu Lawal Auta da Dakta Umma Aminu Inuwa da Dakta Umma Ado Abbas da Dakta Maryam Mansur Yola da Dakta Umma Aminu Inuwa

da kuma Dakta Jibril, da kuma sauran malaman da suka haxa da Malam Muhammad Ammani da Malam Nura Lawan Malam da kuma Malam Muhammad Sulaiman. Haka kuma ina godiya ga xaukacin ma'aikatan Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya na Jami'ar Bayero, Kano.

Haka zalika, ba zan manta da sauran malamaina na wannan sashe da suka amsa kiran mahaliccinmu ba. Wato, Farfesa Mu'azu Alhaji Sani Zariya da Malam Habibu Sani Vavura da kuma Malam Abdulra'uf Tukur. Ina roqon Allah ya jaddada rahmarsa a gare su ya kuma kyautata bayansu. Haka kuma ina godiya ga xaukacin ma'aikatan Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya na Jami'ar Bayero, Kano.

A vangaren abokanan aiki kuwa, ina godiya ga Dakta Aliyu Gadanga Tsafe, Shugaban Babban Xakin Karatu na Jami'ar Tarayya ta Gusau (FUGUS) da Abba Sabo Xantata da Adamu Armaya'u da Sagir Sani Vagwai da Malam Isma'il da Sani Shi'itu Yahuza da Jamilu Bello da kuma Suraja Abdul Gimba da Malam Miftahuddin Abdulqadir Malumfashi da Shamsuddin Muhammad dai sauransu.

Ina godiya ga iyaye da 'yan uwa da abokan arziqi. Daga cikin iyaye, ina godiya ga kakata Hajiya Sadiya Bello Xambatta, ina addu'ar Allah

ya qara mata lafiya. Haqiqa kin nuna min qauna. Haka kuma ina godiya ga Alhaji Umar Alfanda da kuma Alhaji Baffa Usman Maidu da Alhaji Kabiru Balarabe (Sardaunan xan Isa) Hajiya Hauwa Alfanda da Hajiya Jummai Alfanda da kuma Hajiya Murja Alfanda da Hajiya Binta (Mama) da Hajiya Aishatu (Mummy) da Hajiya Binta (Aunty). Ina mai addu'ar Allah ya jiqan sauran iyayena da 'yan uwana da gafara, irin su Alhaji Abdulrahman Alfanda da Alhaji Abdullahi Ahmad (Baba Ubaliye) da Hajiya Hafsatu Alfanda da kuma 'yar uwata Sadiya Ishaq Yusuf da Nusaiba Yusuf Ishaq Yusuf. Sannan ina godiya ga 'yan uwana da suka haxa da Khadija Ishaq Yusuf da Fatima Ishaq Yusuf da Muhammad Ishaq Yusuf da Ramla Ishaq Yusuf da Yusuf Ishaq Yusuf da Umar Mansur da Abdullahi Umar Alfanda da Zubaida Kabiru Balarabe da Aysha Elwakil.

Haka zalika, ina godiya ga Husaini A Alfanda da ASP Sulaiman Aminu Goro da Mahmud Awaisu Abubakar da Jamila Sa'id Muhammad da Aziza da Nusaiba da Shekha da Sajida da kuma Shahida. Ina godiya ga abokanan karatuna da kuma abokanan arziqi, irin su, Husaini Isa Muhammad da Musa Abubakar Kurawa da Hasan Muhammad da Hamza Nuhu da Nafisa Kabir da Hauwa Maikuxi da Hadiza Balarabe Adamu. Ina kuma godiya ga Halima Nasir Dabo da

Malam Isma’il Girei da Malam Abubakar Sirinbai da Malam Jabiru da Malam Muhammad Da’u da dai sauransu. Har wa yau dai, ina godiya ga Malama Fatima Uba Adamu da Malama Aishatu Maimota da Malama Qamariyya. Haqiqa ya zama wajibi na gode wa Malam Kamilu Xahiru Gwammaja, babu abin da zan ce sai Allah ya yi masa sakayya da Aljanna, domin kuwa ya taimaka min qwarai da gaske wajen gudanar da wannan bincike. Haka kuma ina godiya ga Malam Nasir Haris, haqiqa ya cancanci yabo, saboda yadda ya dinga xawainiya da gyara wannan aiki.

A qarshe, ina addu’ar Allah ya saka wa kowa da alheri.

## ABSTRACT

The main objectives of this research is to give an allegorical view of fore- shadowing and suspense manifesting in the *Jiki Magayi*, *Idon Matambayi* and *Ganxoki* novels. In this way, the theoretical frame work generated by Xangambo was used to, technically view the three novels writers strategies to engage their readers attention. The method applied in this study waspurely qualitative in nature.Within this research, many imaginative techniques of fore-shadowing and suspense were discovered in different ways which, their authors used for having an excitement stories which enable them into engaging their readers attention of reading their books. This research also, discovered how fore-shadowing and suspense used in different forms within these novels, like using double and different suspense at same time, and also discovered even in the suspense there is an exaggeration suspense which were used. That to say, what has been discovered stands as a contribution of this research academically, which clearly being a guidance to those have an interest of conducting their research, similarly to this, in other different novels.

## TSAKURE

Kusan a iya cewa nazarin jigo da salo da sarrafa harshe da tsari da yanayin taurari ba baqi ba ne a wajen nazarin qagaggun labarai na Hausa ba, domin kuwa manazarta da dama sun daxe suna ta kai-kawo a kansu ta fuskoki da dama.Saboda haka a qoqarin wannan bincike wajen ba da gudunmawa ga ilmi musamman ta fuskar qagaggun labarai na Hausa ya qudurci fayyace jirwaye na ba-xoki da na xarsau a qagaggun labaran *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki.* Wannan bincike tamkar sauran bincike ne, domin kuwa an bi hanyoyin gudanar da bincike da suka haxa da sigar bincike da matakan qalailaice bincike da kuma tattaunawa da masana da manazarta domin lalubo bakin zaren yadda ya dace a gudanar da wannan bincike.Sa'annan wannan bincike ya ta'allaqa ne ta bin ra'in Xangambo (Jiran bugu) da ke cikin littafinsa na *Gadon Fexe Adabin Hausa* (BBS) A wannan bincike an gano cewa an yi amfani da dabarun ba-xoki da xarsau ta hanyoyi daban-daban don jawo hankalin mai karatu, bugu da qari binciken ya gano shi kan sa xarsau akwai na gangan, haka kuma binciken ya gano yadda marubuta waxannan littattafai suke amfani da dabarar ba-xoki ko ta xarsau a lokaci guda waxanda kuma suke mabambanta don jawo hankalin mai karatu, wanda a qarshe dukkan waxannan abubuwa da wannan bincike ya gano su ne a matsayin gudunmawar wannan bincike ta fuskar ci gaban ilmi da kuma yi wa masu sha'awar gudanar da bincike irin wannan a wasu littattafan daban.

# BABI NA XAYA

# SHARE FAGE

## 1.1 Gabatarwa

Haqiqa an daxe ana gudanar da bincike ta fuskar adabin Hausa, wanda qagaggun labarai na daga cikinsu, domin kuwa masana da dama sun gudanar da bincike da bayar da ta su gudunmawar a ilmance. Daga cikin masanan sun haxa da:

Malumfashi (2006) da Muhammad (2007) Xangambo (2008) da Mukhtar (2008) da Aliyah (2009) Gusau 2009) da Asiyah (2012) . Sai dai na lura da cewa, duk da ire-iren ayyukan da masana suka gudanar a iya sanina ban ci karo da wani bincike kacokan da ya yi qoqarin tattaro dabarun ba-xoki da xarsau ya nazarce su ba. Wannan ya sanya ganin dacewar bayar da gudunmawa ta fuskar zaqulo dabarun ba-xoki da xarsau tare da fayyace su a cikin waxannan zavavvun qagaggun labarai da aka buga su tun a wajen shekarar 1933, saboda irin muhimmiyar rawar da dabarun suke takawa a cikin qagaggun labarai da kuma muhimmancin waxannan littattafai na ga dacewar gudanar da wannan bincike. Na quduri aniyar hakan ne domin bayar da gudunmawa ta hanyar cike gurbin da masana suka bar mana dangane

da abubuwan da suka shafi waxannan dabaru na ba-xoki da xarsau a cikin littattafan nan.

### 1.2 Manufar Bincike

Manufar wannan bincike ita ce fayyace jirwayen dabarar ba-xoki da ta xarsau a cikin littattafan Jiki Magayi da Idon Matambayi da Ganxoki.

Da farko dai idan muka dubi yadda asalin wannan kalma ta jirwaye take, wato jirwaye ko jirwayu za a ga cewa Bahaushiyar kalma ce kamar yadda masana da dama suka yi ittifaqin kasancewarta tsantsar kalmar Hausa. Dangane da hakan ne Hausawa ke amfani da kalmar ta fannoni da dama na maganganunsu na yau da kullum.

Idan aka ce jirwaye kamar yadda maanarsa da aka bayyana a qamusun Hausa (2006) take nufin wani dabbare-dabbaren da ruwan da ya zubo ko ya xigo kan yi wa jikin mutum. Bisa doron wannan maana za a iya fahimtar cewa akwai dabbare-dabbaren ba-xoki da xarsau a cikin waxannan littattafai.

Haka kuma Hausawa na cewa Jirwaye da kamar wanka wanda idan aka yi duba da nazari za a ga cewa a duk lokacin da mutum ya jiqa jikinsa musamman idan da akwai dauxa a jikin bai kuma kai ga yin

wanka gaba xaya ba jikinsa kan yi alamun dabbare-dabbare da ke nuna jirwaye. Ashe ke nan waxannan littattafai qarara akwai jirwayen dabarun ba-xoki da xarsau a cikinsu wanda wannan nazari yake son fayyacewa tare da fito da wuraren da suka yi dabbare-dabbare, wato suka dai jirwayu a cikin waxannan littattafai na Jiki Magayi da Idon Matambayi da Ganxoki.

Haka kuma dabarar ba-xoki, kamar yadda Xangambo (BBS) ya bayyana cewa, ba-xoki na nufin qulla zaren tunanin mai karatu don ya haska wa mai karatu tunanin wani abu da zai iya faruwa a cikin littafinsa a kusa ko nesa, ko kuma abin ba zai faru ba kwata-kwata, domin yakan iya zama na gangan/giri.

Ita kuwa dabarar xarsau, Xangambo (BBS) ya nuna cewa tana nufin sanya wani abu a zuciyar mai karatu a sakamakon littafin da ya karanta, a inda marubuci zai iya jefa tsoro ko baqin ciki ko farin ciki ko kuma mamaki da dai sauransu a zuciyar mai karatu domin ya sami damar jawo hankalinsa a kan littafin da yake karantawa.

Duba da waxannan maanoni da suka gabata za a iya amincewa da cewa Xangambo (BBS) da ya nuna ba xoki da xarsau nauoi ne daga

cikin dabarun jawo hankali da marubuta ke amfani da su, domin kuwa ita dabarar jawo hankali kamar yadda Asiya (2012; Xangambo BBS; Mukhtar 2012; 2014) suka bayyana sun shafi dabarun da mawallafa qagaggun labarai suke da su don jawo hankalin mai karatu dangane da karanta littattafansu ta hanyar jefa masa wani tunani ko xokin ganin faruwar wani abu, wanda yin hakan ne ke ba da damar jan hankalin mai karatu.

Har wa yau kuwa, littattafan Jiki Magayi da da Idon Matambayi Ganxoki littattafai ne da aka wallafa su a sakamakon gasa da aka gudanar a shekarar 1933. Haka kuma littattafai ne masu xauke da gargaxi da faxakarwa da kuma koyar da zamantakewa musamman ta alummar Hausawa da kuma sanya nishaxi a wasu lokuta da dai sauran su.

Dangane da haka ne wannan nazari ya tsayar da tunaninsa kacokan wajen fayyace jirwayen ba-xoki da xarsau a waxannan qagaggun labarai, na Jiki Magayi da Idon Matambayi da Ganxoki duba da muhimmanci da suke da su wajen jawo hankalin mai karatu.

A taqaice dai, manufar wannan bincike ba ta wuce ta zaqulo tare da fito da salon dabarar ba-xoki da xarsau a cikin littattafan Jiki Magayi da Idon Matambayi da Ganxoki, domin a yi nazarinsu da fito da nauoinsu. Daga bisani a fito da yadda kowanne xaya daga marubuta waxannan littattafai ya yi amfani da ba-xoki da xarsau domin jawo hankalin mai karatu.

**1.3 Dalilan Bincike**

Babban dalilin gudanar da wannan bincike shi ne, masana da manazarta da dama sun gudanar da ayyuka a kan jigo da salo da sarrafa harshe da zubi da tsari da yanayin taurari a cikin littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki.* (Bilkisu1998; Dutsin Ma 2002; Fatima 2012; Muhammad 2014; Waziri 2012). Sai dai kash, ba a sami wani nazari a kan waxannan littafai ba da ya ta'allaqa wajen fayyace dabarun ba-xoki da xarsau a cikin littattafan ba. Duk da duba da daxewarsu a nazarin adabin Hausa, tun da an wallafa su tun a shekarar 1933 zuwa yanzu ba a sami wani nazari kacokan da ya fayyace jirwayen ba-xoki da xarsau a cikin littattafan ba.

Har wa yau, duba da yadda waxannan qagaggun labarai suka taka rawa wajen samun nasara a gasar da aka gudanar ta 1933, misali

kamar yadda (Xangambo 2008; Gusau 2009; Malumfashi 2006; Yahaya 1998) suka tabbatar da haka. Ga shi kuma har a waxannan lokuta ba a manta da su ba da yadda suke ilmantarwa da wayar da kan al'umma musamman ta yadda suke qulla zaren dabarar tunaninsu domin fito wa da mai karatu wata rayuwa da take yi masa jagora wajen aiwatar da rayuwa mai kyau da kuma gargaxi da sauran abubuwa na faxakarwa da wayar da kai, nag a dacewar na bi diddigin ganin yadda suka yi amfani da dabarun ba-xoki da xarsau a cikin littattafansu.

Haka zalika, idan muka kalli cewa duk da yawaitar ayyukan masana a cikin waxannan qagaggun labarai, hakan bai sa ni cin karo da wani bincike da ya qalailaice waxannan dabaru ba a cikin waxannan littattafai ba, wanda hakan ya sake ba ni qwarin gwiwar aiwatar da nawa binciken a cikinsu, duk da dai yawancin Hausawa sun gamsu da cewa "Duniya juyi-juyi ce wai kwaxo ya faxa ruwan zafi". Abin nufi a nan shi ne, ba wai ana nufin tilas ne ko naqasu ne ga manazarta ba da suka shuxe, wato ana nufin givi ne da suka bar wa na baya. Hakan bai rasa nasaba da dai faxin Hausawa na cewa " Da na gaba ake gane

zufin ruwa", wato dai da ayyukansu ne na gano wani givi da suka bari, kenan dai da bazarsu ake rawa.

A wani qaulin kuwa, an sami kwaranyar ayyuka na Muhammad (2007) da ya yi maganar ba-xoki a littafin So aljannar duniya da na Aliyah (2009) da ta fayyace ba-xoki da xarsau a ayyukan R.M East. Akwai kuma aikin Asiyah (2012) wadda ta kalli ba-xoki da xarsau a littafin Magana Jari ce na 1 da na 3. Inda gizo ke saqar shi ne, baicin waxannan ayyukan manazarta, kawo yanzu ban ci karo da da wasu nazarce-nazarcen da aka yi kacokan a kan ba-xoki da xarsau ba, daxin daxawa waxannan ayyuka na Muhammad (2007) da na Aliyah (2009) da Asiyah (2012) sun daxa ba da wani givi ne gare ni wajen fayyace jirwayen ba-xoki da xarsau a littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki* , domin kamar yadda bayani ya gabata su sun kalla ne a matanin wasu littattafai daban ba waxannan ba.

Sai dai kash, ga shi dai nan gida kaxan ne suka yi nazari a kan ba-xoki da xarsau, sai dai sauran al'ummu na duniya sun daxe suna baza komarsu a kan waxannan ayyuka. Misali Strong (1996) wani Baturen Amurka da ya bayyana dabarar xarsau da kuma yadda marubuta ke amfani da ita wajen sanya tunanin masu karatu cikin kokwanto a kan

wani abu da aka ba su labari, wato dai sukan sanya mai karatu a cikin yanaye-yanaye daban-daban da kuma tambayar kansa da kansa a kan ta yaya hakan zai faru ko kuma mene ne dalilin da ya sa haka ya faru, da dai sauran abubuwa na xarsau a zuciyar mai karatu. Haka kuma ya kawo misalin dabarar xarsau a wani matani da yake nuna faruwar wani abu da kuma xarsa tunani a zuciyar mai karatu.

Daxin daxawa kuma, Blawn (1998) Wannan shi ma na daga cikin Turawan qasar Amurka da ya gina ayyukansa a kan ba da shawarwari ga marubuta dangane da amfani da dabarun jawo hankali, inda ya nuna muhimmancin dabarun da kuma yadda ya dace marubuci ya zama mai qirqira ta hanyar yin amfani da labari mai xauke da abubuwan da za su sanya farin ciki ko tausayi ko mamaki, wato dai dukkan wasu dabaru da za su haifar da samuwar wani yanayi a zuciyar mai karatu, haka kuma ya bayar da misali a kan wata rubutacciyar waqa mai xauke da abubuwa masu xarsuwa a zuciyar mai karatu waxanda suke xauke da farin ciki da tausayi da ma wani abu mai motsa rai na baqin ciki da dai sauran su.

Bugu da qari, Booth (2005) na daga cikin Turawan qasar Amurka da ya gina ayyukansa a kan siffofin yadda ake so mawallafi ya kasance mai qirqira a koyaushe, dangane da haka ya bayar da misali na wani labari mai xauke da mamaki da tausayi da farin ciki da dai sauran su. Har ila yau dai, akwai da yawa daga cikin manazarta Turawa da suka bayar da gudunmawarsu ta fuskar gina ayyukansu a kan abubuwan da suka shafi dabarun jawo hankali daban-daban, waxanda wasu dabarun sun shafi ba-xoki ne wasu kuma sun shafi xarsau kai tsaye da dai sauran su.

Daga cikin wasu manazarta Turawan da suka yi wannan qoqari akwai irin su Kirszner da Mandell (2007) waxanda su ma Turawa ne na qasar Amurka da suka gina ayyukansu a kan abin da ya shafi qa'idojin rubuta qagaggun labarai ta yadda suka fayyace yadda dabarun jawo hankali suke tare da kawo misalai daga wasu labarai masu xauke da dabarun ba-xoki da xarsau a cikinsu. Haka su ma sauran waxannan manazarta na Turawa sun gina ayyukansu ta hanyoyi daban-daban tare da bayyana muhimmancin da dabarun jawo hankali suke da su da kuma nuna cewa babu wani littafi da za a qirqira wanda ba shi da waxannan dabaru na ba-xoki da xarsau a cikinsa. Daga cikinsu sun haxa da Applebee (2006) da Odell (2007) da Higdon (2009) da

Brewer (2013) da dai sauran su.Ga shi dai su al'ummu na duniya sun yi qoqari wajen aiwatar da ayyuka a kan su, sai dai mu a nan manazarta ba su yi musu cincirindo ba, wato sun yi musu riqon sakainar kashi tun da dai manazarta ba su bayar da muhimmanci a kan su ba, musamman littattafan da aka rubuta na Hausa.

Awani qaulin kuma, Xangambo (BBS) ya bayyana cewa ba-xoki a qagaggun labarai takan zamanto dabara ce da marubuta qagaggun labarai suka fi amfani da ita wadda ke ba da hasken akwai abin da zai faru gaba,kuma marubuta sukan qulla zaren tunaninsu ta hanyar jan tunanin mai karatu a kana bin da zai faru gaba, ta hakan ne mai karatu zai shiga karakainar ba-xokin gangan/giri ko nag aske/tabbas a kan abin da zai auku a cikin lokaci mai tsayi ko gajere.

A wani qauli kuma, Xangambo (BBS) yana ganin marubuta kan xarsa wa mai karatu tunanin da zai motsa masa rai ta sigar tausayi ko fargaba ko mamaki ko baqin ciki ko murna ko zuga ko qara gishiri da dai sauransu. Bisa doron hakan ne marubuta qagaggun labarai kan yi amfani da dabarar xarsau ta sigar qirqira da jan hankali wadda ke sanya zuciyar mai karatu a cikin wani hali na qaqa-ni- ka yi wadda a gaba za a iya kawar da tunanin mai karatu ta hanyar cusa masa wani

abu a zuciyarsa wanda bai zama daidai da abin da ya xauka daga farko ba, ta haka ne wannan bincike ke ganin muhimmanci da alfanu da dabarar ba-xoki da xarsau take da ita da jirwayensu a cikin matanin qagaggun labarai ba abubuwa ne da qarara za a yi wa riqon sakainar kashi ba.Wannan bincike ya faxi riqon sakainar kashin ne ta la'akari da cewa yawancin binciken da ake gudanarwa sukan fi ta'allaqa ne a kan abin da ya shafi jigo da salo da sarrafa harshe, wanda ga magani a gonar yaro, sai dai tun daga lokacin da aka fara nazarce-nazarce a iya cewa ba a kai ga fito da dabarun ba-xoki da xarsau a cikin waxannan littattafai ba, wanda hakan na iya haifar da cewa ba don wannan bincike da aka gudanar ba, da ba a sami wani bincike a kusa wanda zai mayar da hankali wajen fayyace waxannan dabaru a cikin waxannan littattafai ba, wato tamkar sun zama allura ce a cikin ruwa. Wannan na nufin cewa, dukkannin bayanan da aka yi a sama, suna tabbatar da dalilin gudanar da wannan bincike, bai wuce ganin fa'idar da ba-xoki da xarsau suke da ita ba, da kuma yadda masana musamman na harshen Hausa suka bar givi game da gudanar da wani bakandamen nazari wanda ya qunshi waxannan dabaru na ba-xoki da xarsau a cikinsa.

Wani dalili da ya sanya gudanar da wannan bincike shi ne, sha'awar da nake da ita game da karatun qagaggun labarai na Hausa, ita ta sake yi min qaimi wajen zavar wannan hanya ta bincike game da sa-xoki da xarsau da marubuta ke amfani da su, domin samun damar isar da saqonsu.

## 1.4 Muradun Bincike

Kamar yadda aka bayyana daga farko an gina manufar wannan bincike ne domin a fayyace dabarar ba-xoki da ta xarsau a littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki*. Ke nan muradan wannan bincike sun ginu a kan:

*1.* Fito da ire-iren ba-xoki da xarsau a cikin littttafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki*
2. Bayar da gudunmawar ilmi ta fuskar nazarin ba-xoki da xarsau.
*3.* Gano hanyoyin da marubuta waxannan qagaggun labarai suka bi wajen qulla zaren tunaninsu, don jawo hankalin mai karatu.
*4.* Fayyace yadda aka yi amfani da ba-xoki da xarsau a cikin littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki*.

## 1.5 Tambayoyin Bincike

1. Ba-xoki da xarsau na daga cikin nau'o'in salon jawo hankalin mai karatu. Shin ta yaya za a gano yadda aka yi amfani da waxannan dabaru a cikin littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki*?

2. Waxanne gudunmawa ake ganin nazarin ba-xoki da xarsau za su bayar a ilmance ?

3. Shin ko akwai wani nazari da aka gudanar wanda ya dogara gaba xaya a kan ba-xoki da xarsau?

4. Waxanne irin kalmomi ne ko jimloli waxanda da zarar an cire su ake rasa ba-xoki da xarsau a cikin labari?

### 1.6 Farfajiyar Bincike

Kamar yadda Qamusun Hausa (2006:135) ya nuna farfajiya na nufin cewa wani xan fili bayan an wuce soro kafin a shiga tsakar gida. A iya cewa, farfajiyar wannan aiki ba ta wuce fayyace jirwayen dabarar ba-xoki da ta xarsau a cikin littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki* ba. Daga cikin farfajiyar wannan bincike an waiwayi wasu ayyuka da aka gudanar a kan ba-xoki da xarsau inda aka fahimci su dai nau'o'i ne na dabarun jawo hankali. A bisa tsarin bincike kuwa za a ga cewar su waxannan littattafai sun ta'allaqa ne a kan qagaggun labarai na *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki.*

### 1.7 Ra'in Bincike

Haqiqa a kowanne nazari irin wannan, ana sa ran a aiwatar da shi ne a bisa wani ra'i da aka bayyana hanyoyi da qa'idojin da ake bi a gabatar

da nazari wanda ya dace da ra'in da za a xora aikin a kansa. A wannan bincike da aka gabatar, an gina shi ne a bisa ra'in Xangambo mai suna “Dabarun Nazarin Qagaggun Labarai” da ke cikin littafinsa mai suna *Gadon Fexe Adabin Hausa* jiran bugu. Dangane da qunshiyar wannan ra'i ya kawo bayanai dangane da dabarun jawo hankali da marubuta suke amfani da su, daga cikin dabarun ya kawo ba-xoki, a inda ya bayyana cewa dabara ce wadda akan ba mutum haske cewa wani abu zai faru a gaba. Wannan ra’i ya bayyana cewa aikin wannan dabarar ba-xoki ita ce sa mai karatu xokin ya ci gaba da karatu don ya ga abin da zai faru. A cikin wannan ra’i an bayyana cewa bisa jumla ba-xoki iri biyu ne, wato ba-xokin gaske dogo ko gajere da kuma ba –xokin giri ko na gangan. Wannan ra’i na Xangambo ya bayyana ma’anar ba-xoki kamar haka:

> Wannan dabara ce da marubuta labarai suka fi amfani da ita. Ba-xoki, ko kuma abin da wasu kan kira “Sa-xoki”, ko “tushe” dabara ce wadda akan ba mutum haske cewa wani abu zai faru a gaba. Aikin wannan dabara shi ne ta sa mai karatu xokin ya ci gaba da karatu don ya ga abin da zai faru.

Bisa wannan ma’ana da aka kawo za a iya bayyana ba-xoki da cewa, dabara ce ta marubuta domin qulla alaqar tunanin mai karatu da

saqon da marubutan suke son isarwa. Wato marubuta kan qulla dabarar jan hankalin mai karatu ta hanyar nuna masa wani abu mai muhimmanci da mai karatu zai so ya ji yadda ta kasance a gaba. Wato idan mai karatu ya ci gaba da bibiya zai iya tarar da ba-xokin nan a kusa ko kuma nesa, ko kuma xungurungum ba zai sami wannan ba-xokin a cikin littafin ba, ke nan ya zama ba-xokin gangan.Haka kuma an kawo ire-iren ba-xoki a cikin wannan ra'i da bayyana nau'o'in ba-xoki kamar haka:

Xangambo (BS) ya bayyana ire-iren ba- xoki kamar haka:

> Ba-xoki, bisa jimla iri biyu ne. Akwai "ba-xokin gaske ko na tabbas, kuma akwai "ba-xokin giri ko ba-xokin gangan". Ba-xokin gaske shi ne wanda marubuci yake ba da hasken cewa abu zai auku kuma ya auku xin. To amma shi wannan ba-xokin gaske ko na tabbas, akwai dogo akwai gajere. Dogon ba-xokin gaske shi ne wanda daga inda aka ba da hasken abu zai auku, ba zai auku xin ba sai bayan lokaci mai tsawo. Shi kuwa gajeren ba-xokin gaske shi ne wanda da an ba da hasken abu zai auku sai ka ga ba a daxe ba abin ya auku.
>
> To amma shi ba-xokin giri ko na gangan shi ne wanda aka nuna wa mai karatu cewa wani abu zai auku, amma har aka gama labarin abin bai auku ba. Yawanci irin wannan ba-xoki na gangan akan kawo shi ne kawai don ya xaga hankalin mai karatu, ya kwaxaita masa cewa wani abu zai auku don

> kawai a sa sha'awar mai karatun ta xore. To amma wani lokaci marubucin ne yakan manta.

Wannan ra'i na Xangambo (BBS) ya kawo bayanai dangane da xarsau a matsayin dabarar jawo hankalin makaranci. Inda ya nuna cewa akan xarsa wa mai karatu tunanin da zai motsa shi dangane da tausayi ko tsoro da fargaba da ban haushi da murna da baqin ciki da zuga da qara gishiri da dai sauransu kamar haka:

> Xaga hankali wata dabara ce da marubuta ke amfani da ita, domin su sami damar isar da saqonsu cikin armashi.
>
> Marubuci kan qirqiro wani abu da zai motsa tunanin mai karatu, hankalinsa ya xaga ta fuskoki daban-daban. Irin wannan xaga hankali kan qunshi: Ba mai karatu tsoro da motsa tsikar jikinsa, ko sa shi murna, ko ban haushi ko takaici, ko mamaki, ko na ban dariya, ko qara gishiri da sauransu.

Bisa doron wannan ma'ana da aka kawo, a iya cewa:

> Xarsau shi ne zavin wata hanya da marubuta suke yi don su sanya zuciyar mai karatu a cikin wani hali na xan wani lokaci, wanda a gaba za a iya kawar da tunanin mai karatu ta hanyar cusa masa wani abu a zuciyarsa, wanda ba lallai ya zama iri xaya da na farko ba, sai dai shi ma na xan wani lokaci ne.

Daga cikin irin abubuwan da marubuta kan sanya a zuciyar mai karatu sun haxa da:

> Tausayi ko farin ciki, ko kuma baqin ciki ko wani abu da zai sanya raha a zukatan masu karatu

Haka kuma daga cikin nau'o'in xarsau akwai waxannan:

- Amfani da tasirin addini
- Hoton zuci
- Raha/Ban dariya
- da dai sauransu.

### 1.7.1 Dangantakar Ra'in da Binciken

Wannan ra'i na da alaqa da wannan bincike. Domin kuwa ta hanyar yadda aka fayyace tare da kawo ma'anar waxannan dabaru ne aka sami hasken yadda aka gudanar da wannan bincike. Don haka, wannan bincike alaqarsa da ra'in ita ce jagorancin sanin dabarun da kuma yadda ake iya fahimtarsu a cikin kowanne littafi. Hakan ne ya bayar da dama ta zaven wasu littattafai don a gudanar da bincike a fito da ire-iren ba-xoki da xarsau da aka yi amfani da su, tare kuma da fayyace su da duba yanaye-yanayensu.

## 1.8 Tarihin Marubuta Littafin *Jiki Magayi*

Aliya 2009 ta kawo tarihin R.M East in da ta bayyana cewa: An haifi Rupert Moltrie East a birnin London da ke qasar Ingila a shekarar (1898). Ya yi karatunsa na Firamare a makarantar Dragon School da ke Oxford, sannan ya sami takardar shaidar kammala karatun gaba da Firamare a makarantar Sa Edward da ke Oxford a shekarar (1916). (Aliya, 2009: 20-25).

An turo Mr. East Nijeriya, inda ya yi wa ma'aikatar ilimi aiki. Dakta East ya kula da yankuna waxanda suka haxa da yankin Benuwe, inda ya duba makarantun da ke garuruwan Katsina Ala da Abinsa da Keffi da garin Makurxi da yankin Adamawa, sai yankin Arewa maso gabas, a inda aka tura shi Kwalejin horon malamai ta Katsina a matsayin malami mai koyar da yanayi da labarin qasashe.A Kwalejin horon malamai ta Katsina ne Dokta East ya koyar da wasu fitattun 'yan Nijeriya kamar su Abubakar Imam da Abubakar Tafawa Valewa. (Aliya, 2009: 25-28).

Haka kuma an tura Dakta East Zariya a qarqashin hukumar kula da ilmin manya. Bayan an buxe hukumar fassara a shekarar (1929) a Kano an mayar da ita ofishinta na dindindin Zariya, a shekarar (1929)

aka mayar da Dokta East ofishin.Bayan xan lokaci Dakta East ya shirya tare da shugabantar gasar shekarar (1933), wanda Daraktan ilmi na jihar Arewa ya xora nauyin gudanar da ita kan hukumar fassara.

Dakta East ya kasance xaya daga cikin waxanda littattafansu suka lashe wannan gasar da nasa mai suna "*Jiki Magayi"*. Sannan Dokta East da Alhaji Abubakar Imam sun sake samar da littafi mai suna "Qara*min Sani". (*Aliya, 2009: 28-31).

Dakta East ya auri wata Bafulatanar Adamawa mai suna Hajiya Dada Sare, kuma ta zauna da shi tsawon zamanin da ya yi a Arewacin Nijeriya. Daga qarshe Dokta East ya koma tare da ita Ingila bayan ya yi ritaya. A tsawon zamansu Allah bai ba ta haihuwa ba, ta rasu a shekarar (1974).

Dakta East ya sake auren Bafaranshiya Misis Naeyer, wadda ta rasu a shekarar (2007). Kuma suna da 'ya'ya biyu da Dokta East, mace da namiji, Jean da Michael. Dokta East ya mutu ranar 3, ga watan Yuni, 1975 a asibitin Princes Margaret, Swindon da ke Ingila. Ya rasu yana xan shekara (72), ya bar matar aure xaya da 'ya'ya biyu. (Aliya, 2009:36-39).

Fatima 2012 ta bayyana cewa : An haifi John Tafida Umar a shekarar (1903) a unguwar Wusasa a ci kin Zariya. Sunan mahaifinsa Makama Umaru, shi kuwa Bafulatanin Borno ne asalinsa. Sunan John Tafida na gaskiya (Abbas).

Ya fara karatun allo a wurin mahaifinsa,ya kai kimanin izifi arba'in, daga baya mahaifinsa ya bayar da shi ga wani jami'in addinin Kirista mai suna Dr.Millar a wajen shekarar (1910).

A wurin Dr. Millar ya fara karatun boko har ya sami ilimi mai zurfi wanda ya kai kusan na Midil a wancan lokaci. Daga nan ya fara aiki a sashen ilimi na lardin Zariya, sai ya koma Hukumar fassara har zuwa (1945) ya riqe muqamin jami'i mai lura da kayayyakin ma'aikatar Gaskiya Coorporation Zariya.

A shekarar (1955) zuwa (1956) ya koma N.E ta Zariya da aiki inda ya riqe muqamin wakilin raya qasa.

Daga nan aka naxa shi xan Galadiman Zazzau, kuma hakimin Zangon Kataf. A cikin wannan lokaci ya ce ya dawo musulunci, amma daga baya ya ce ba zai iya ba. Bayan an dawo Wusasa an naxa shi Sarkin Wusasa a (1966), ya sake dawowa Gaskiya Coorporation inda ya riqe muqamin akanta. Tafida ya rubuta littafin "*Jiki Magayi"* a lokacin da

aka sa gasar rubuta littattafan zube a shekarar (1933), kuma littafinsu ya zama xaya daga cikin littattafan da suka lashe wannan gasar. Kamar yadda bayan hukumar talifi ta tace littattafan da suka samu nasara, sai ta sanya matsayinsu a na biyar kamar yadda jerin sunayen yake a tsare (Yahaya, 1988).

Tafida ya rasu ranar 31, ga watan Agusta na (1982). (Fatima, 2012) a cikin (Gwarzo, J.M (2002):3-4.

### 1.8.1 Tarihin Marubucin Littafin *Idon Matambayi*

An haifi Malam Muhammadu Gwarzo a garin Gwarzo a shekarar (1911). Ya yi makarantar Lardi Ta Kano daga shekarar (1923).

Malam Muhammadu Gwarzo ya yi aiki a ma'aikatar ruwa a matsayin Sufiritanda na Kano N.A a shekarar (1923-1936). Haka kuma ya yi aiki N.A a shekarar (1936-1944). Sannan ya zama malamin makaranta ta Midil daga (1939-1944). Sannan ya zama mai kula da ilmin manya a lardin Kano daga (1952-1956).

A shekarar (1963-1969), ya zama babban sakataren ofishin madaki.Kuma ya zama Kansila mai kula da horar da ma'aikata daga (1969-1975). Daga (1975-1980) ya zama kwamishina na dindindin a

hukumar kula da qananan hukumomi. (Fatima, 2012) a cikin (Gwarzo, BB).

Malam Muhammadu Gwarzo ya zama xaya daga cikin waxanda suka shiga gasar rubutu na qagowa a shekarar (1933), kuma littafinsa yana xaya daga cikin littattafan da suka lashe gasar mai suna "*Idon Matambayi"*. Malam Muhammadu Gwarzo ya rasu ya bar mata biyu da 'ya'ya bakwai a watan Fabrairu (1992). (Fatima, 2012) a cikin (Gwarzo, BB).

**1.8.2 Tarihin Marubucin Littafin *Ganxoki***

An haifi Muhammad Bello a shekara ta (1890) a Kagara ta qasar Tegina. Mahaifinsa shi ne Alqalin Kagara a wancan lokaci.

Muhammad Bello ya yi karatu a gida gun mahaifinsa. Walin Katsina ya yi aiki da N.A (Native Authority) ta Katsina, daga shekarar (1914-1921) a matsayin malamin makaranta. A shekarar (1921-1945) ya yi aiki a Kwaleji ta Katsina, sannan ya sake komawa N.A ta Katsina daga (1945-1971).

Walin Katsina ya sami karramawa a matsayinsa na xaya daga cikin xaliban makarantar farko da aka buxe a (1908), wato makarantar Xan Hausa.

An karrama Walin Katsina a matsayin xaya daga cikin wakilai na qasar Ingila, wato M.B.E, (Member of the British Empire) a (1938). Bayan ya yi ritaya a (1945) aka zave shi a matsayin babban alqali a Katsina a 10 ga watan Satumba. (1954) aka zave shi Walin Katsina.

Ya rasu a kan wannan matsayi na Walin Katsina ranar 21 ga watan Nuwamba, 1971. Ya rasu ya bar mata biyu da 'ya'ya goma sha biyar, tara maza, shida mata, da jikoki da dama.

Muhammad Bello ya zama xaya daga cikin waxanda suka shiga gasar shekarar (1933), kuma littafinsa na daga cikin waxanda suka lashe wannan gasar mai suna "*Ganxoki*" (Fatima, 2012) a cikin (Muhammad,1989:16) da (Mora, 1989:308).

### 1.9 Kevavvun Kalmomi da Taqaitattun Kalmomi

1. Fore-shadowing : Ba-xoki -

> Baxoki ita ma kalma ce da Xangambo (BS) ya qirqiro ta, domin ta zama xaya daga cikin dabarun jawo hankali a qirqirarrun labarai.Baxoki dai dabara ce da marubuta qirqirarrun labarai suke yi, a inda suke bayar da haske kan wani abu da zai iya faruwa a gaba, amma wannan abu zai iya kasancewa ya qi faruwa. Saboda haka Baxoki dabara ce ta shafo kan wani al'amari a cikin labari,a xan takalo wa mai karatu zancen, to amma idan tafiya-ta yi-tafiya wannan xan batu da aka takalo zai iya faruwa a kawo shi tar-tar-tar, a bayyana yadda abin ya faru. Haka kuma za a iya samun akasin haka, wato abin nan da aka

takalo wa mai karatu aka nuna zai faru a samu bai farun ba.An fi samun wannan dabara ta baxoki a cikin qagaggun labarai. Asiya (2012 :189 ).

2. Suspense: Xarsau -

> Xangambo(1995:252-3) a cikin Aliyah (2009:88) ya bayyana ma'anar xarsau da cewa :
>
> "Xaga hankali wata dabara ce da marubuta ke amfani da ita, domin su sami damar isar da saqonsu cikin armashi.

Marubuci kan qirqiro wani abu da zai motsa tunanin mai karatu, hankalinsa ya xaga ta fuskoki daban-daban. Irin wannan xaga hankali kan qunshi: Ba mai karatu tsoro da motsa tsikar jikinsa, ko sa shi murna, ko ban haushi, ko takaici, ko mamaki, ko na ban dariya, ko qara gishiri da sauransu."

3. Allegory: Jirwaye - Qamusun Hausa :219, ya bayyana cewa jirwaye na nufin : Dabbare-dabbaren da ruwan da ya zubo kan yi wa jikin mutum ko bango.

5. Text: Matani – Qamusun Hausa: 339 ya bayyana cewa matani na nufin : Littafin da ba a yi wa sharhi ba.

6. Novel: Qagaggun Labarai- Mukhtar 2004:11 ya bayyana cewa:

> “Idan aka ce rubutun zube ana nufin rubutun da ba waqa ba, ba kuma wasan kwaikwayo ba. Zube na

> nufin tsagwaron rubutu kai tsaye wanda aka yi shi cikin shafi ko shafuka da sakin layi daban-daban, a rubuce ko a maganance, wato ta hanyar magana."

6.BBS – Wannan taqaitattun kalmomi ne da suke nufin babu shekarar wallafa.

### 1.10 Naxewa

A wannan babi an kawo gabatarwa da manufar bincike da dalilan bincike da muradun bincike da farfajiyar bincike da tambayoyin bincike da ra'in bincike da dangantakar ra'in da binciken da tarihin marubuta qagaggun labaran *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki* da kevavvun kalmomi da taqaitattun kalmomi.

# BABI NA BIYU

# BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA

## 2.1 Gabatarwa

Wannan babi ya qunshi bitar ayyukan da suka gabata waxanda suke da alaqa da wannan bincike, waxanda aka tattaro daga kundayen bincike da bugaggun littattafai..

## 2.2 Ayyukan Magabata

Strong (1996:170) ya nuna cewa, marubuci, a kodayaushe qoqarinsa shi ne bin hanyoyin da zai jawo hankalin mai karatu. Dangane da hakan ne, yake amfani da xarsau wanda zai dace da tsarin da aka gina labara a kansa. A wannan littafi an nuna yadda amfani da xarsau a cikin littafi yake da muhimmanci, domin kuwa da xarsau ne manufar saqon kowanne littafi take kammaluwa. An lura da cewa, marubucin wannan littafi ya yi bayani dalla-dalla a kan xarsau daban-daban da ake samu a cikin littattafai, da kuma yadda suke taka rawa wajen fahimtar saqon da ke cikin kowanne. Wannan littafi ya taimaka mini tare da yi mini jagora ta yadda na daxa fahimtar xarsau da yadda marubuta daban-daban suke amfani da shi a cikin littattafansu.

Applebee (1997:345) ya bayyana cewa marubuta qagaggun labarai na da wata baiwa da suke da ita ta fuskar qawata labaransu don jawo hankalin masu karatu. Domin kuwa ya bayyana cewa daga cikin ire-iren waxannan dabaru na marubuta don jawo hankalin mai karatu akwai xarsa wa mai karatu a ransa waxansu abubuwa masu iya faruwa a rayuwa ta zahiri. Sai dai ya nuna cewa akan tsarma da kawo wa mai karatu wani abu da ba lallai ne ya kasance a rayuwa ta zahiri ba, ya bayar da misali da cewa, zai iya kasancewa a bayyana wani labari mai nuna wata dabba na magana,amma wanda hakan ba abu ba ne mai faruwa a rayuwa ta zahiri. Applebee (1997) ya daxa bayyana yadda marubuta ke amfani da xarsau daban-daban don jawo hankalin mai karatu, ya nuna yadda marubuta suke kawo wasu xabi'u a cikin littattafansu, waxanda suka sava da abin da ke iya faruwa a zahirin rayuwa. Hakan zai sanya xarsau na ban mamaki a zuciyar mai karatu, da dai sauran dabarun da marubuta kan iya amfani da su wajen jawo hankalin mai karatu. Akwai dangantaka da binciken da nake gabatarwa ta fuskar yadda ya ambaci yadda marubuta suke shirya dabaru don jawo hankalin mai karatu, har ya nuna cewa suna amfani da xarsau domin su shirya labarin da duk wanda ya karanta shi zai jawo hankalinsa. Bambancin shi ne, bincikena ya duba yadda

waxansu marubuta qagaggun labarai suka yi amfani da dabarun ba-xoki da xarsau ne a cikin littattafansu. Wannan littafi ya taimaka min qwarai wajen daxa fahimta da kuma jagora a kan dabarun jawo hankalin da marubuta qagaggun labarai ke amfani da su don su cim ma burinsu na jawo hankalin masu karatu.

Blau (1998:56) ya yi bayanin yadda marubucin littafi ya dace ya tsara labarinsa. A inda ya bayyana cewa shi labari ya danganta ne daga zavin marubuci a kan abin da yake so ya tsara labari, inda ya bayyana cewa wasu marubutan sukan fara tunanin wata matsala ne da za su gina tunanin labaransu a kanta, wanda ta hanyar hakan ne za su sami damar xarsa abubuwa daban-daban a zuciyar mai karatu don jawo hankalinsa. Haqiqa wannan littafi na da alaqa da nawa binciken ta fuskar yadda ya bayyana dabarar xarsau, daga cikin matakan da marubuta ke amfani da su domin jawo hankalin masu karatu, sai dai bambancin binciken da wannan littafi shi ne, yadda bincikena ya zavi wasu qagaggun labarai da ya gudanar da yadda aka yi amfani da dabarun ba-xoki da xarsau a cikinsu. Ba shakka littafin ya taimaka min da kuma jagora wajen gudanar da wannan bincike.

Booth (2005:123) ya nuna cewa, akwai waxansu muhimman ababen lura a bisa yadda marubuta qagaggun labarai ke tsara labarai. Akan samu cewa akwai muryar mawallafi wanda ba kai tsaye mai karatu ke samun labarai ba, ma'ana yana samun labarin ne ta hannun muryar mawallafi ko kuma ta hannun tauraron littafin. Haka kuma ya bayyana a cikin littafinsa, cewa a dukkan tsarin qagaggen labari, ana samun wata madogara da za ta sanya mai karatu tunanin yadda wani lamari yake faruwa a cikin labari, ko kuma wanda zai faru a gaba a cikin labarin. Bugu da qari kuma, ya nuna cewa qagaggun labarai tamkar bayyana wa mai karatu hoton wani abu ne ta hanyar siffanta shi da kuma kwatancensa, wanda hakan ke zama xarsau ga mai karatu. Wannan littafi ya taimaka da yi mini jagorar yadda na daxa fahimtar yadda ya dace na gudanar da nawa binciken na fito da dabarun ba-xoki da xarsau a cikin littattafan da na gudanar da bincike.

Kiyawa (2006) ya bayyana salon rubutun mawallafa littattafan da ya gabatar da nazarinsu bisa dangantakar da take akwai a tsakaninsu ta fuskoki da dama da suka haxa da: salon rubutunsu ta fuskar gina labarai da zaven kalmomi da amfani da ranakun ko kwanan wata da dai sauransu.

Kiyawa ya kawo bambancin da ke tsakanin marubuta ta fuskar amfani da adon harshe, musamman kamantawa da kuma dalilan rubuta littafi da suka haxa da ilmantarwa da shugabanci da faxakarwa da dai sauransu. Haka kuma ya bayyana dabarun jawo hankali a cikin littattafan ta hanyar amfani da hoto da kalmomin jan hankali da kalmomin aro da na azanci.Wannan kundin bincike na Kiyawa na da alaqa da aikina ta fuskar qagaggun labarai da kuma shan inuwa xaya ta adabi. Bugu da qari, bincikensa ya shafi salo ne, haka ni ma nawa binciken yana da alaqa da salo, ta fuskar ba-xoki da xarsau.Binciken na kiyawa ya zama jagora ga aikin da zan gabatar don ya daxa fahimtar da ni yadda ya dace na aiwatar da nawa aikin binciken.

Thomas (2006:92) ya yi cikakken bayani ne game da xarsau, domin kuwa ya nuna cewa marubuta qagaggun labarai kan jefa shakku da tambayoyi masu ximbin yawa a ransu, a duk lokacin da suke karanta wani littafi. A inda ya bayyana cewa wani mai karatun yakan sami kansa da jin a ransa cewa da shi ne tauraro a cikin littafin da bai aikata wani abu da bai yi masa daxi ba a ransa, wannan ke nuna yadda marubuta ke qoqarin saqa zaren tunaninsu ta hanyar sanya wani abu a zuciyar mai karatu da ya danganci tsarin marubucin. Haka kuma marubuci kan iya xarsa wa mai karatu mamaki wanda har bayan gama

labarin zai tsaya a zuciyar mai karatu. Wannan littafi na da alaqa ta kusa da wannan kundin bincike, haka kuma ya zamar min jagora da qara haskaka min hanya wajen fahimtar xarsau.

Muhammad (2007)ya duba dabarun da aka bi wajen shirya labari game da salon aiwatarwa ta fuskar dabarun jawo hankali da suka haxa da: ba-xoki sa-xoki da kuma xarsau da hange da waiwaye. Haka kuma nazarin nasa ya duba abin da ya shafi sarrafa harshe a cikin littafin waxanda ya bayyana su kamar haka: Nagartar kalmomi da sababbin kalmomi da kuma kalmomin aro da kuma qarin bayani a kan dabarun jawo hankali musamman na siffantawa, wato hoto cikin gurbi. Wannan bincike na Muhammad (2007) na da alaqa da bincikena, domin nazarin nasa ya bayyana dabarun jawo hankali na ba-xoki da xarsau. Sai dai bambancin shi ne, bincikensa ya yi nazarin salo ne gaba xaya a wani littafi, inda nawa binciken ya taqaita a kan dabarun ba-xoki da xarsau a cikin wasu qagaggun labarai. Wannan bincike na Muhammad (2007) ya taimaka min da kuma yi min jagora wajen aiwatar da nawa binciken.

Yakasai (2007) ya kawo ma'ana da ire-iren rubutun zube da hanyoyin nazarin qagaggun labarai.Yakasai ya kawo taqaitaccen tarihin

mawallafi da kuma jigon littafin da ya yi nazarinsa, daga nan ya kawo sharhi a kan salon littafin da duba dabarun jawo hankali da kuma salo da sarrafa harshen littafin da nazari a kan taurarin cikin littafin da ire-iren taurari.

Wannan aiki na da alaqa da aikina,domin shi ma ya kawo dabarun jawo hankali a cikin littafin da ya yi nazari, bambancin da ke tsakani shi ne, shi ya yi sharhin littafi ne guda xaya, a inda ya nazarci salon mawallafin, ni kuwa aikina ya yi nazari ne a kan ba-xoki da xarsau.

Muhammad (2011)ya yi tsokaci a kan jigo da qananan jigogin da suka qunshi cin amana da qaddara da soyayya da quruciya da kuma rashin imani.Haka kuma ta fuskar abin da shafi zubi da tsari da salo da sarrafa harshe, an yi bayaninsu a cikin wannan kundin bincike na Muhammad.

Dangane da salo kuwa, Muhammad (2011) ya kawo sharhi game da salon littafin na filla-filla da duba dabarun jawo hankali a cikin littafin da dabarun sarrafa harshe da kuma bayanin taurari da kuma qimar jimilla na littafin da ya gabatar da nazarin a kansa. Aikin Muhammad na da alaqa da aikina ta fuskar abin da ya shafi batun salon dabarun jawo hankali, wanda shi ma ya kawo su a cikin nazarin da ya gabatar

na littafin da ya yi nazari, sai dai akwai bambanci a tsakanin nawa aikin da na gabatar da nasa, saboda nazarinsa a littafi xaya na *Duniya Budurwar Wawa* ne, ni kuma nazarina da na gabatar ya qunshi salon ba-xoki da xarsau ne a littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki*

Wannan aiki nasa ya matuqar haskaka min hanya wajen gudanar da aikina da kuma qara fahimtar da ni yadda ya dace a gabatar da nazari irin wannan.

Kirszner da Mandell (2007:341) sun bayyana cewa marubuta qagaggun labarai, kan shirya yadda wani lamari zai faru a cikin labaransu, ta hanyar kawo wani labari mai ruxani da rikitarwa wanda zai iya sanya xarsau a zuciyar mai karatu. Ke nan, marubuta na amfani da dabarun xarsau ta hanyar shirya wani labari da zai haifar da afkuwar xarsau a cikin littattafansu, ta hanyar kawo labari mai ratsa zuciya, mai xauke da rikicin da zai zama sanadiyyar jawo hankalin mai karatu ta hanyar xarsau.Har wa yau dai, sun sake bayyanawa a cikin littafinsu cewa, marubuta qagaggun labarai kan shirya wata dabara da take haskaka wa mai karatu faruwar wani lamari a gaba, wanda zai so faruwar hakan, wato ba-xoki kenan. Wannan littafi na da

alaqa da bincikena, sai dai sun bambanta ta fuskar tsarin littafinsu, da nawa binciken. Wannan littafi ya taimaka da yi min jagora wajen daxa haska min yadda na gudanar da nawa binciken.

Odell (2007:186) ya bayyana matakai daban-daban na dabarun da marubuta ke amfani da su don jawo hankalin mai karatu. Daga cikin matakan sun nuna cewa, marubuci da farkon farko shi ne ya dace ya fara tsara wani tunani, wanda zai yi rubutu a kansa, wanda da zarar wannan labari ya bayyana zai zama mai jan hankali ga mai karatu. Wannan manazarci ya qara da dewa, daga cikin matakai na qirqiro labari sai an haxa da wasu dabaru da za su sanya mai karatu zaquwar tambayar kansa cewa mene ne abin da zai faru a gaba idan ya ci gaba da karanta littafi. Ke nan wannan abin da zai xarsu a zuciyar karatu shi ne zai zama ya jawo hankalinsa dangane da wannan labari. Kai tsaye za a iya bayyana cewa daga cikin waxannan matakai da wannan marubuci ya bayyana akwai ba-xoki da xarsau. Wannan ne ya haifar da alaqa da nawa aikin da kuma daxa yi min jagora wajen gudanar da nawa binciken.

Aliyah (2009) ta gabatar da nazari da sharhi kan wasu zavavvun ayyukan Dr. East, wanda daga cikinsu akwai littafin *Jiki Magayi*, a

inda ta yi sharhin littafin tun daga kan jigo, da zubi da tsari da salo da sarrafa harshe, da kuma ambaton dabarun jawo hankali kamar su ba-xoki da xarsau da amfani da hotuna da zane- zane a cikin nazarin da ta gabatar. Sa ‘annan kuma ta yi nazari da sharhi kan wasan kwaikwayon nan na "The Six Hausa Plays".Akwai alaqa da aikin da Aliyah (2009) ta gabatar da nawa, ta fuskar mawallafi da littafin da ta yi nazari da sharhi a kansa. Musamman ta yadda ta yi bayani da kawo wasu dabarun jawo hankali na wasu vangarori na cikin littafin *Jiki Magayi.* Bambancin aikin Aliyah (2009) da nawa shi ne, ita kai tsaye ta duba tarihin rayuwa da ayyukan Dr. R.M East a fannin harshen Hausa, da kuma yin nazari da sharhi kan wasu vangarori na dabarun jawo hankali a cikin littafin na *Jiki Magayi.* A inda nawa aikin da na gabatar, kai tsaye aka nazarci ba-xoki da xarsau da aka yi amfani da su a cikin wannan littafi na *Jiki Magayi.*

Higdon (2009:8) ya bayyana ba-xoki a matsayin dabarar da marubuta suke amfani da ita don jawo hankalin mai karatu. Haka kuma ya nuna cewa kusan ana samun wannan dabara ba a cikin qagaggun labarai kaxai ba, har da wasannin kwaikwayo ana samun ta. A wannan takarda ta Higdon (2009) ya yi bayani game da waiwaye a cikin labarai da kawo misalai na yadda ake qulla dabarun jawo hankalin

mai karatu. Wannan takarda na da alaqa da aikina da na gabatar ta fuskar bayanai a kan dabarar jan hankali ta ba-xoki , sai dai akwai bambanci ta fuskar yadda bincikena ya karkata da kuma inda takardarsa ta sanya gaba. Wannan takarda na xaya daga cikin abubuwan da suka taimaka mini wajen haska mini yadda na gudanar da nawa binciken a kan ba-xoki da xarsau, domin dukkan bayanan takardar sun yi qarin haske ne a kan ba-xoki.

Asiya (2012) ta yi nazarinta ne game da salo da sarrafa harshe, inda aikin nata ya qunshi fuska biyu. Fuska ta farko ita ce yadda ta qalailaice dabaru iri daban-daban da aka yi amfani da su a cikin littafin da ta yi nazari. Waxannan dabaru sun haxa da dabarar ba-xoki da xarsau da dai sauransu. Dangane da fuska ta biyu ta wannan bincike sun qunshi dabarun sarrafa harshe da aka yi amfani da su, waxanda suka haxa da azancin magana da amfani da daidaiton lafazi da karin harshe da zaven kalmomi a cikin zube.Wannan kundin bincike na da alaqa da bincikena ta fuskar ba-xoki da xarsau. Sai dai kuma sun bambanta ta fuskar littattafan da na gudanar da bincikena da nata littafin, da kuma yadda bincikena ya faxaxa nazari a kan ba-xoki da xarsau, da kawo abubuwan da a nata binciken ba ta kawo su ba,

game da ba-xoki da xarsau. Binciken nata, ya qara min haske da jagora wajen hanyar da na bi don gudanar da nawa binciken.

Brewer (2013:193) ya bayyana xarsau da cewa dabara ce da marubuta suke amfani da ita wajen qoqarin sanya nishaxi ko akasin haka a zuciyar mai karatu. Wannan manazarci ya bayyana cewa marubuta sukan zavi ire-iren xarsau da suke son gina labarinsu da su, wato xarsau da zai fi mamaye littafi da kuma dacewa da tsarin yadda aka gina labari. Sa'annan ya ci gaba da kawo wasu matsaloli da akan iya fuskanta dangane da amfani da xarsau a cikin littafi, domin kuwa kowanne mai karatu ya bambanta da xan 'uwansa, ta la'akari da cewa abin da ya yi wa wani daxi ya sanya shi cikin farin ciki game da wani littafi da ya karanta, ba lallai shi ne abin da zai yi wa xayan mai karatu daxi ba a zuciyarsa.Wannan takarda kai tsaye na da alaqa da bincikena dangane da yadda aka kawo bayanai da suka danganci xarsau, sai dai akwai bambanci ta fuskar yadda kowannenmu bincikensa ya sanya gaba. Haka kuma takardar ta daxa haska mini yadda na gudanar da bincikena a kan ba-xoki da xarsau.

Xanja (2013) ya yi qoqarin fito da salon da marubuta qagaggun labaran da aka yi nazari a kansu suke amfani da harshe,da yadda suke

zaven kalmomi da kuma yadda suke sarrafa kalmomin da ma amfani da nau'o'in jumloli a cikin littattafan da aka gudanar da wannan nazari a kansu.

Baya ga haka, binciken Xanja na qunshe da ma'anar salo da ta harshe daga wajen masana,haka kuma ya kawo tarihin samuwar qagaggun labarai na Hausa da taqaitaccen tarihin marubutan da ya yi nazari a cikin littattafansu.

An yi qoqarin gano kamanci da bambanci da tasirin da harshe yake da shi, dangane da fahimtar marubuci, musamman abin da ya shafi zavin kalmomi da sarrafa su, domin su ne tamkar tubalan ginin labari. Wannan aikin bincike yana da alaqa da nawa aiki da zan gabatar, ta fuskar salo. Wannan bincike ya qara ba ni hasken yadda na gudanar da nawa binciken a kan ba-xoki da xarsau.

Binta (2014) ta yi qoqarin kawo ma'ana da ire-iren salo da ma'anar kwatantawa.A wannan nazari an kawo tarihin mawallafa littattafan da aka gabatar da nazari a cikin littattafansu, da kuma bayani a kan amfani da harshe a cikin salo da salon littattafan guda biyu, ta fuskar amfani da rukunan nahawu wajen ginin jumla.

Binta ta kawo tsarin yadda aka yi amfani da wasu kalmomin da rukunan nahawu da suka haxa da : Suna da byanau da sifa da yanayin tsarin ginin jumla, haka kuma ta kawo kwatancin da ke tsakanin littattafan da ta yi nazarinsu guda biyu, ta kawo kwatancin ne ta fuskoki da dama da suka haxa da: Amfani da suna da bayanau da sifa da dai sauran kwatancin da ke tsakanin littattafan guda biyu.Haka kuma ta kawo bayani na bambancin salon amfani da harshe tsakanin littattafan da ta gabatar da nazarin nata a kansu.

Wannan kundin bincike haqiqa ya zama mai fa'ida a gareni da kuma yi min jagora a bisa aikin da na gabatar na jirwayen ba-xoki da xarsau a littattafan *Jiki Magay*i da *Idon Matambayi* da *Ganxoki.*

Habiba (2014) ta kwatanta salo da sarrafa harshe a rubutacciyar waqa da kuma qagaggen labari.A cikin wannan nazari an bayyana ma'anar salo da nau'o'insa da ma'anar sarrafa harshe, da kuma yadda salo da sarrafa harshe suke tasiri a cikin wallafa.Salon waqar Mikiyar Zuhudu ta vangaren dabarun sarrafawa da suka haxa da kwatantawa da siffantawa da jinsintarwa da dai sauransu. An yi nazarin kamanci da bambancin salo na gaba xaya a waqar Mikiyar Zuhudu da littafin Mace Mutum.

Wannan nazari na Habiba na da alaqa da aikina da na gabatar, musamman ita ma nazarin nata ya tavo salo da sarrafa harshe, sai dai ita nata nazarin ya qunshi rubutacciyar waqa da kuma qagaggen labari, inda nawa nazarin ya duba ba-xoki da xarsau.

Qamariyya (2018) ta yi kwatancin waxansu littattafai guda biyu. Binciken nata ya tavo wasu dabarun jawo hankali kamar su xarsau da ba-xoki da amfani da addini da kuma amfani da zane ko hoto da dabarun sarrafa harshe. Bayan dukkan waxannan dabarun jawo hankali da ta yi magana a kansu, sai kuma ta yi qoqarin kwatanta dabarun a tsakanin littattafan da ta yi nazari, a inda ta fito da kwatancinsu ta fuskar fifiko ko daidaito ko kashi da dai sauransu. Wannan bincike nata yana da alaqa da binciken da na gabatar ta fuskar yadda ta yi cikakkun bayanai game da dabarun ba-xoki da xarsau. Sai dai bambancinmu shi ne, nawa binciken ya duba ba-xoki da xarsau a waxansu qagaggun labarai, inda nata binciken kuwa ya fi mayar da hankali wajen kwatanci a tsakanin qagaggun labarai na *Ta cuce ni* da *Saba xan Sabi*. Babu shakka wannan bincike na Qamariyya (2018) ya taimaka tare da yi mini jagora wajen yadda na gudanar da nawa binciken ta fuskar daxa fahimtar ba-xoki da xarsau. Wanda daga tsanin nata ne da na sauran manazarta na sami dammar hango abin da

ba su fito da su ba, ni kuma bincikena ya yi qoqarin fitowa da su a cikin binciken da na gudanar.

### 2.3 Naxewa

A wannan babi an kawo bitar ayyukan da suka gabata, waxanda suka taimaka da yi mini jagora wajen gudanar da wannan bincike.

# BABI NA UKU

# DABARUN GUDANAR DA BINCIKE

## 3.0 Gabatarwa

Wannan babi ya qunshi dukkan waxansu hanyoyi da dabaru da aka yi amfani da su, wajen gudanar da wannan bincike. Daga cikin waxannan dabaru da aka yi amfani das u, akwai waxannan :

## 3.1 Sigar Bincike

Wannan bincike da aka gudanar, ya bi tsarin labartaccen bincike ne, wato, dukkannin sharhin da binciken yake yi, ana yin sa ne a labarce. Kenan, an bi tsarin sharhantaccen bincike ne kamar yadda (Creswell 2009; da Dornyei 2011; da Tavakoli 2012; da Muhammad 2017; a cikin Aisha, 2018) suka bayyana. Daga jin siga ta labartaccen bincike an san abu ne da ya shafi labari da kuma sharhi. Binciken ya yi amfani ne da sigar xaukar matanin labari daga cikin littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki,* waxanda suka jirwayu da dabarun jawo hankali na ba-xoki da xarsau, sa'annan a yi sharhin misalan ba-xoki ko xarsau da aka samu a cikin kowanne xaya daga cikin waxannan littattafai. An bi wannan siga ne domin ta taimaka wajen fito da

sauran ba-xoki da xarsau da manazarta da yawa da suka shuxe ba su waiwaye su ba.

### 3.2 Matakan Gudanar da Bincike

A wannan bincike an yi amfani da matakai mabambanta waxanda suka zama ginshiqi kuma abin lura kafin a aiwatar da shi. Da farko dai daga cikin matakan gudanar da wannan bincike sai da aka sami damar mallakar waxannan littattafai na *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki* ta hanyar sayen biyu daga ciki a kantin sayar da littattafai na Jami'ar Bayero a cikin shekarar 2018. Haka kuma an sami xayan littafin na *Idon Matambayi* ta kafar sadarwa ta Intanet daga hannun Malama Fatima Uba Adamu, wadda ita kuma ta tabbatar da cewa ta same shi ne daga hannun Farfesa Abdallah Uba Adamu. Bayan an sami waxannan littattafai ne, aka duqufa wajen nazarinsu, da fito da ba-xoki da xarsau a cikinsu.

Bayan karance-karancen waxannan littattafai sai aka fitar da dabarun ta sigar rukuni-rukuni, wanda hakan ne ya ba ni dama wajen gwaggwama su domin isar da bayanai a yayin da wannan bincike ke qoqarin tabbatar da yadda zai ba da gudunmawa ga ilmi. Hakan ya sa na ziyarci xakunan karatu na Jami'ar Bayero Kano, a shekarar 2017,

wato babban xakin karatu na Jami'ar, da kuma xakin karatu na Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya. Har ila yau, na ziyarci xakin karatu na Sashen Harsuna da Al'adun Afirka na Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya, a shekarar 2017. A dai wannan shekara ta 2017 a qoqarin gudanar da wannan bincike, na ziyarci xakin karatu na Jami'ar Usmanu Xanfodiyo da kuma Jami'ar Tarayya da ke Gusau.

Haka zalika, wannan bincike ya ba ni dama ta tattaunawa da masana da manazarta, waxanda daga kaxan daga cikinsu, akwai Farfesa Abdulqadir Xangambo, wanda aka tattauna da shi ranar Litinin 3rd,Yuli, 2017, domin kuwa ta hannunsa ne aka sami cikakkun bayanai game da ba-xoki da xarsau. Bayan nan an sami nasarar tattaunawa da Farfesa Isa Mukhtar ranar Laraba,12th ga watan Yuli, 2017, da kuma Dr. Halima A Xangambo, ranar Alhamis, 3rd, ga watan Agusta,2017. Sa'annan an tattauna da Farfesa Ibrahim Garba Satatima, ranar Laraba 23 ga watan Agusta na shekarar 2017.

### 3.3 Samfurin Bincike

Wannan vangare ne mai xauke da wasu matakai masu fayyace vangaren da mai karatu ya karkata wajen samun bayanai da kuma

sarrafa su ta hanyar sharhi ko tarke a nazarinsa. (Creswell, 2009; Dornyei, 201; Muhammad, 2017; Tavakoli, 2012 a cikin Aisha, 2018)

Dangane da bin hanyar waxannan masana ne kuwa, za a yi karatun waxannan littattafai a tsanake, daga nan kuma a zayyana vangaren da bincike ya karkata ta hanyar tattaro bayanai da kuma sarrafa su. Wannan bincike ya yi la'akari da abubuwan da zai nazarta sa'annan ya qididdige su daki-daki kamar yadda suke a wannan jadawali.

**Jadawalin Ba-xoki da Xarsau a Littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki***

| S/No | Sunan Marubuci | Sunan littafi | Adadin ba-xoki |
|---|---|---|---|
| 1 | R.M East da John Tafida | *Jiki Magayi* | Guda goma (10) |
| 2 | Malam Muhammadu Gwarzo | *Idon Matambayi* | Guda biyar (5) |
| 3 | Malam Bello Kagara | *Ganxoki* | Guda shida (6) |

An kawo wannan jadawali ne domin ya sauqaqa wa wannan bincike gano yadda aka yi amfani da ba-xoki da xarsau, da gane adadinsu da

kowanne marubuci na waxannan littattafai da aka yi nazari a cikinsu ya yi amfani da ba-xoki ko xarsau.

### 3.4 Makamashin Bincike

Idan aka ce makamashi a bincike, ana nufin wani abu da mai bincike ya dogara a kansa. Wato abin da idan babu shi za a iya cewa kai tsaye babu bincike. Makamashin da ya hasa wutar wannan bincike bai wuce littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki* ba, domin ta kansu ne aka bi aka fito da waxannan dabaru na ba-xoki da xarsau.

### 3.5 Hanyoyin Tattara Bayanan Bincike

A wannan bincike an bi hanyoyi da dama da suka bayar da damar samun nasarar wannan bincike. Daga cikin hanyoyin da aka yi amfani da su kuwa, su ne kamar haka :

Ziyartar xakunan karatu manya da qanana na Jami'o'I irin su Jami'ar Bayero ta Kano da kuma Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya, da kuma Jami'ar Usmanu Xanfodiyo ta Sakkwato. Dukkannin waxannan xakunan karatu an samu damar ziyartarsu domin sanin makamar yadda binciken ya gudana.

Daga cikin hanyoyin tattara bayanan bincike kuwa, an tattauna da masana daban-daban don lalubo bakin zaren gudanar da wannan bincike. Masanan da aka sami damar tattaunawa da su, sun haxa da Farfesa Abdulqadir Dangambo wanda aka tattauna da shi ranar Litinin 3rd,Yuli, 2017, domin kuwa ta hannunsa ne aka sami cikakkun bayanai game da ba-xoki da xarsau. Bayan nan an sami nasarar tattaunawa da Farfesa Isa Mukhtar ranar Laraba,12th ga watan Yuli, 2017, da kuma Dr. Halima A Xangambo, ranar Alhamis, 3rd, ga watan Agusta,2017. Sa'annan an tattauna da Farfesa Ibrahim Garba Satatima, ranar Laraba 23 ga watan Agusta na shekarar 2017.

Waxannan su ne hanyoyin da aka bi wajen tattara bayanan wannan bincike.

### 3.6 Qalailaice Bayanan Bincike

A yayin qalailaice bayanan wannan bincike, an yi amfani da matakin sharhi ne wajen qalailaice jirwayen da aka samu dangane da ba-xoki da xarsau a littafin *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki.* Abin nufi a nan shi ne, dukkan sharhin da aka yi da kuma fito dab a-xoki da xarsau da yadda suka wakana a cikin waxannan qagaggun labarai, su ne qalailace bayanan bincike.Haka kuma an bi hanyoyi na fito da

yadda za a fahimci ba-xoki ko xarsau cikin sauqi, ta hanyar nuna yadda marubutan ke amfani da kalmomi da jimloli masu xauke da ba-xoki da xarsau.

**3.7 Xa’ar Gudanar da Bincike**

Haqiqa kowanne bincike na da tsari da kuma xa’ar yadda ake gudanar da shi. Dangane da xa’ar gudanar da aka yi amfani da ita wajen gudanar da wannan bincike , an bi tsari na koyon darasi a fannin adabin Hausa a Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya a Jami’ar Bayero na kusan tsawon shekara xaya. Daga nan ne kuma aka fara fafutukar neman qa’idar cikasa wani vangare na samun digiri na biyu a fannin na Hausa. An bi qa’ida ta neman izini daga Sashen koyar da Harsunan Nijeriya. Sa’annan kuma aka fara rubutu na gabatar da takardar neman izinin gudanar da bincike da kuma sake gabatar da takarda ta neman cikasa wata qa’ida ta samun digiri na biyu. Haka kuma wannan bincike ya sami jagorancin duba aiki daga wajen jagoran duba aiki, daga bisani kuma aka matsa zuwa mai duba aiki na cikin gida, da kuma mai duba aikin daga waje. A taqaice dai waxannan su ne abubuwan da xa’ar wannan bincike ya qunsa.

### 3.9 Kammalawa

A wannan babi an bayyana hanyoyi da dabarun da aka yi amfani da su wajen gudanar da wannan bincike. An kawo sigar bincike da matakan bincike da kuma makamashin bincike. Haka kuma an kawo qalailaice bayanan bincike da xa'ar gudanar da bincike.

# BABI NA HUXU
# SALON JAWO HANKALI NA BA-XOKI DA XARSAU A LITTATTAFAN *JIKI MAGAYI* DA *IDON MATAMBAYI* DA *GANXOKI*

## 4.1 Gabatarwa

Wannan babi shi ne ginshiqin wannan bincike. Haka kuma an fayyace ba-xoki da xarsau da nau'o'insu da yanaye-yanayensu da kuma muhimmancinsu a cikin waxannan littattafai na *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da kuma *Ganxoki*.

## 4.2 Fayyace Nau'o'in Ba-xoki a Littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki*

A nan ana nufin cewa, an kawo nau'o'in ba-xoki da xarsau ne da kuma tantance nau'o'insu ta hanyar kawo su kamar haka:

- Ba-xoki
- Ba-xokin gaske na kusa/ na nesa
- Ba-xokin gangan/giri
- Xarsau
- Xarsau na ban dariya
- Xarsau na ban tausayi
- Xarsau na ban takaici
- Xarsau na ban mamaki
- Xarsau na farin ciki
- Xarsau 'yan tagwai
- Xarsau na gangan

Dalilin da ya sanya fayyane waxannan nau'o'i na ba-xoki da xarsau shi ne, domin su yi jagora ga wannan bincike. Domin kuwa ta hanyar ne za a gane dukkan wani nau'i na ba-xoki ko xarsau da aka yi amfani da su a cikin wannan bincike.

## 4.3 Tarken Matanonin Ba-xoki da Xarsau a Littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki*

Wannan littafi na *Jiki Magayi* an yi amfani da ba-xoki daban- daban a cikinsa. Sai dai shahararriyar dabarar ba-xoki da marubucin ya fi yawaita amfani da ita a cikin littafinsa ita ce dabarar ba-xokin gaske na nesa, domin ita ce dabarar da yake ganin za ta dace da tsarin littafinsa ta kuma sanya hankalin mai karatu karkata ga inda ake so ya dosa. Haka kuma baya ga wannan dabara ta ba-xokin gaske na nesa marubucin ya yi amfani da ba-xokin gaske na kusa da kuma ba-xokin gangan jefi-jefi a cikin wannan littafi.

### 4.3.1 Ba-xokin Gaske na Kusa

A nan, an sanya wa mai karatu ba-xokin ganin yadda za ta kasance ga Abubakar a yayin da yake shirin karvar saqo daga wajen Tausayinka-da sauqi, inda aka ce:

Sai ya sa hannu cikin ratayensa, ya ce:

> Ga wannan ka kai masa, da ganinta ya sani. In ka tafi ka gaya masa dukkan labarina ka ce ina gaishe shi ina kuwa da rai. Ina kuwa so ya yafe mini dukan irin dangin abin da na yi masa *(Jiki Magayi, sh.14)*.

Wannan batu da marubucin littafin nan ya takalo wa da mai karatu, ba-xoki ne na gaske kuma na kusa. Domin kuwa tun a shafi na (14), an ga inda Tausayinka-da sauqi ya ba wa Abubakar saqo zuwa ga mahaifinsa, kuma ya ciro laya ya ba shi wadda zai nuna wa mahaifinsa. Haka kuma ba tare da vata lokaci ba mai karatu ya karanta Abubakar ya xauki hanya zuwa wajen baban Tausayinka- da sauqi.Wannan ke nuna mana cewa ba-xoki ne na gaske na kusa. Dangane da abubuwan da suka haifar da wannan ba-xoki kuwa, su ne kalmomi da jimlolin da marubucin ya yi amfani da su. Domin kuwa daga an cire su, za a ga cewa babu ba-xokin. Misali:

- Ga wannan ka kai masa
- Da ganinta ya sani
- Ka gaya masa dukkan labarina
- Ka ce da shi ina so ya yafe mini dukan dangin abubuwan da na yi masa.

> Waxannan na daga cikin jimlolin da suka haifar da zaquwar mai karatu na son ganin hakan ya faru.

Mai karatu a nan, zai so ganin yadda wannan al'amari zai faru, domin kuwa ga shi Malam Shaihu ya sanya za a kirawo masa malami don a fassara masa mafarkin da ya yi, inda marubucin yake cewa :

> Da haka ya farka daga barci, duk jikinsa na rawa, ya yi ta wasuwasin wannan abu cikin ransa har gari ya waye. Da asalatun fari ya aika aka kira masa wani malamin qasa. Da ya zo ya ce yana so ya ba shi labari. Malamin ya share qasa ya buga, ya ce, " Na ga maganar aure da kuwa haihuwa tsakani, na ga wani kuma ya qwace gabanka, amma idan ka maida hankali za ka ture shi *(Jiki Magayi, sh.* 2).

Wannan ba-xoki ne na gaske kuma na kusa. Dalilan da suka haddasa faruwar ba-xokin su ne, jimlolin da marubuci ya yi amfani da su kamar haka:

- Na ga maganar aure da kuwa haihuwa tsakani.

- Na ga wani kuma ya qwace gabanka.

- Amma idan ka maida hankali za ka ture shi.

Waxannan jumloli su ne qashin bayan haifar da wannan ba-xoki, domin kuwa da zarar an cire su, za a ga cewa babu wani abu da zai jawo hankalin mai karatu. Marubucin wannan littafi ya takalo wa mai karatu batun auren Malam Shaihu da Zainabu. Sa'annan ya nuna yadda Abubakar ya sha gaban kowa a wajen Zainabu, da kuma yadda aka sanar da Malam Shaihu cewa matuqar ya yi qoqari zai ture Abubakar. Wannan batu da aka takalo zai sa mai karatu son ganin yadda za ta kasance tsakanin Malam Shaihu da Zainabu, da ma yadda shi Malam Shaihu zai ture Abubakar. Haka kuwa aka yi, domin ba da jimawa ba ne mai karatu ya ga yadda al'amura suka sauya, domin kuwa, Malam Shaihu ya ture Abubakar, don haka wannan ba-xoki ne na gaske na kusa.

Marubucin wannan littafi na nuna wa mai karatu cewa mahaifiyar Kyauta za ta koma asalin garinsu da zama. Haka kuma tabbas mai karatu zai so ganin faruwar komawarta ko akasin haka. Wannan ya sanya aka haska wa mai karatu da kuma takalo masa da zancen kamar haka:

Sai ya yi sallama, ya tashi. Bai xauki kome daga cikin gidan ubansa ba,ko guzuri, ya tafi Kwanci tashi har ya kai Garuje. Ya tafi wurin

uwarsa ya gaya mata dukan abin da ya faru Ya ce, “Yanzu ya kamata in koma da ke gida, Ki yi zamanki can cikin danginki” *(Jiki Magayi,* sh. *50).*

Wannan ba-xokin gaske ne na kusa, domin mai karatu zai so ya ga ko mahaifiyar Kyauta za ta amince ta koma gida ko kuwa, sai dai ba ta qi amincewa da maganar xanta ba Kyauta, ta bi shi ya je ya mayar da ita cikin gidan mahaifinsa a garin Galma. Haqiqa idan aka yi la’akari da waxannan jumloli da marubucin ya yi amfani da sum za a ga cewar su ne suka sanya mai karatu zumuxin ganin faruwar haka. Waxannan jumloli su ne kamar haka :

-Yanzu ya kamata in koma da ke gida.

- Ki yi zamanki can cikin danginki.

Daga jin waxannan jumloli, za a fahimci cewa su ne aka yi amfani da su, domin jawo hankalin mai karatu. Wannan ne ke nuna mana ba-xokin na gaske ne na kusa, wanda marubucin littafin ya yi amfani da shi a qarshen littafinsa don jawo hankalin mai karatu.

A littafin *Idon Matambayi* an yi amfani da wannan dabara ta ba-xokin gaske na kusa, kuma ta daxa taimaka wa wajen fahimtar saqon wannan littafi. A nan, mai karatu zai ga cewa jama'a sun taru don su je

su duba su ga inda mavoyar varayin nan suke, a nan mai karatu zai so ganin yadda za ta kasance kamar haka:

> Manyan gari suka yi shiru. Chan wani ya che, " Ranka ya daxe, yanzu abin da za mu yi sai ka sa a yi shela, dukan wanda ya sani da shi xanfarauta ne ya zo, da kuma tsofon mayaqi. Idan sun zo mu hau dawaki mu bi hanyar Dutsen Sauke- mu- raba, inda Sani ya che wataqila suna nan, tun bai mutu ba *(Idon Matambayi,* sh. 33).

Wannan shi ma ba-xoki ne na gaske, saboda dai Sarki ya amince da shawarar da wani daga cikin jama'arsa ya bayar, a kan cewa a yi shela a haxu da jarumai don a je a gano inda ake zaton a nan varayin da suke zuwa Kafi sata suke. Wannan batu da aka takalo wa da mai karatu na shawarar manyan gari, ba a jima ba sai aka tabbatar da aiwatar da wannan shawara. A nan mai karatu zai ga cewa an zo wajen da ake tsammanin a nan ne su Idon Matambayi suke, duk da dai ba a sami nasarar kama su ba a wannan lokaci. Don haka wannan ya tabbatar da cewa ba-xoki ne na gaske kuma na kusa, jumlolin da marubucin ya yi amfani da su da suka sanya aukuwar wannan ba-xoki su ne kamar haka:

- Idan sun zo mu hau dawaki.
- Mu bi hanyar Dutsen Sauke- mu- raba, inda Sani ya che wataqila suna nan, tun bai mutu ba.

Waxannan jumloli su ne suka sanya mai karatu bin diddigi don ganin abin da zai faru a gaba. A nan, marubucin wannan littafi ya yi qoqarin haska wa mai karatu cewa akwai wani abu da zai faru a gaba, domin kuwa xaya daga cikin qananan taurari ya ci alwashin ramuwar abin da sauran varayi suka yi masa, misali inda aka ce :

> Batsokana ya yi mamaki yana chewa a zuciyarsa, "M mhm! Ni Batsokana na yi wa kaina, mutanen nan Dauke da Kwache da Idon Matambayi sun kyauta.Suka zo suka yi sata suka tafi suka bar ni. Amma da ikon Allah sai mun haxu, ko ba daxe ko ba jima" *(Idon Matambayi,* sh. 41).

Haqiqa wannan ba-xoki ne na gaske na kusa, saboda mai karatu zai so ya karanta ko alwashin nan da Batsokana ya ci na cewa ko ba daxe ko ba jima za su sake sake haxuwa zai tabbata ko akasin haka. Za a iya cewa ya tabbata don ya sake haxuwa da su,duk da cewa sun yi savani da Idon Matambayi wanda bayan an raba dukiyarsu ta sata ya xauki alqawarin komawa gida da kuma daina yin sata, wannan ne ya haifar da savani a tsakaninsa da Batsokana. Abin da ya haddasa aukuwar wannan ba-xoki kuwa, su ne jumlolin da marubucin littafin ya yi amfani da su kamar haka:

- Amma da ikon Allah sai mun haxu, ko ba daxe ko ba jima.

Waxannan jumloli su ne za a iya fahimtar ba-xokin da marubucin wannan littafi ya yi amfani da su cikin sauqi, ta yadda da zarar an cire su, za a sami cewa babu wannan ba-xoki.Wannan shi ne ba-xokin da marubucin ya kammala littafinsa da shi, wanda idan muka lura za mu ga cewa marubucin ya fara da ba-xokin gaske na kusa, kuma shi ya fi yawaita amfani da shi a cikin littafinsa, haka nan da shi ya kammala wannan littafi.

Mai karatu zai so ganin yadda al'amari zai kasance, musamman rashin aiwatar da abin da Idon Matambayi ya yi niyya a kan varawon nan. Ga shi kamar haka :

> Da tsayawarsa sai ya che, "Ka yi mini sutura, don Allah kada ka kashe ni sai na ga xanuwana wanda muka baro a kwanche" Idon Matambayi ya yarda, suka koma *(Idon Matambayi,* sh. 3)

A nan marubucin wannan littafi, ya jawo hankalin mai karatu da takalo masa da zancen komawa zuwa wajen xan 'uwan varawon nan da suka haxu da Idon Matambayi. Wannan batu da aka takalo wa mai karatu an cika shi, domin an ga inda suka koma can wajen da suka bar xan 'uwan wancan varawon a kwance. Za a fahimci wannan ba-xoki ne cikin sauqi ta yadda aka yi amfani da waxannan jumloli kamar haka:

- Ka yi mini sutura, don Allah kada ka kashe ni.

- Sai na ga xanuwana wanda muka baro a kwanche.

Waxannan su ne jumlolin da za su sanya mai karatu qoqarin bin yadda za ta kasance a cikin wannan labari. Wannan ke nuna cewa ba-xoki ne na gaske kuma na kusa.

A wannan ba -xoki za a ga cewa, xaya daga cikin varayin ya nuna damuwarsa a kan rashin dawowar xaya daga cikinsu. Haqiqa a nan an jawo hankalin mai karatu ne don ya ci gaba da karanta littafin, sai dai mai karatu zai damu da sanin halin da varawon ya shiga da abin da ya hana shi dawo wa gida, misali inda aka ce:

> Da isarsu gida sai suka iske shi qulle. Idon Matambayi ya tambaya da mamaki, "A'a! Xauke bai dawo ba har yanzu, lafiya dai?" Qwace ya ce, "Kai, ba kome an jima ka gan shi. Amma tun da muke tare bai tava yin dare irin na yau ba." Suka buxe qofa suka shiga, suka zauna suna jiran Xauke Qatoqato, ba su gan shi ba har kusan tsakar dare. Idon Matambayi ya sake cewa, "Yau me ya sami Xauke, Ko an kama shi ne?" *(Idon Matambayi*, sh.13).

Akwai ba-xokin gaske na kusa a wannan shafi, dalili kuwa shi ne yadda marubucin ya yi amfani da wasu jumloli masu nuna ba-xoki cikin sauqi kamar haka:

- Idon Matambayi ya tambaya da mamaki.

- "A'a! Xauke bai dawo ba har yanzu, lafiya dai?"

- Qwace ya ce, "Kai, ba kome an jima ka gan shi.

- Suka zauna suna jiran Xauke Qatoqato, ba su gan shi ba har kusan tsakar dare.

- Idon Matambayi ya sake cewa, "Yau me ya sami Xauke,

- Ko an kama shi ne?

Waxannan jumloli na daga cikin abubuwan da suka haddasa aukuwar wannan ba-xoki da ya jawo hanlin mai karatu, domin da zarar an cire su, za a ga babu wannan ba-xoki. A nan, mai karatu zai so ganin dawowar xaya daga cikin varayin nan ko akwai wani dalili da ya sanya faruwar hakan, musamman yadda xaya daga cikin varayin yake qarfafa wa Idon Matambayi gwiwa a kan cewa Xauke zai dawo. Sai dai har suka yi bacci suka farka bai dawo ba, daga nan ne kuma ba da jimawa ba sai ga shi ya bayyana. Wannan ke nuna cewa ba-xokin

gaske ne na kusa mai nuna darasi a rayuwarmu ta yau da kullum a kan cewa, dukkan wanda zuciyarsa ta mutu yake neman hanyar sata a rayuwarsa, to haqiqa ba shi da kwanciyar hankali a rayuwarsa.

A nan, mai karatu dai ya karanta abin da ya faru a tsakanin tsoho da Ganxoki, har ga shi tsohon ya taimaka wa Ganxoki da kayan yaqi. Haqiqa mai karatu zai so ganin abubuwan da aka bayyana cewa kayan yaqin za su taimaka ko akasin haka, ga yadda ta kasance kamar haka :

> Ya kawo wani kulki, ya ba ni, ya ce, "Ko dutse ka daka da shi ya tsage, kome girmansa. Ga takobi Shafau, kome ka sara da shi ya karye, kome maridancin aljani, ya bi ka. Ga sanda, idan ka girgiza ta, qararta kamar aradu ce, sai tartsatsin wuta ya riqa fita yana kashe mutane" (*Ganxoki*, sh. 20).

Marubucin wannan littafi ya bayyana wa mai karatu cewa wani tsoho ya taimaki babban tauraro da wasu kayan yaqi kamar kulki da takobi mai suna shafau. Marubucin ya yi amfani ne da wasu jumloli masu xauke da wannan ba-xoki kamar haka :

- Ko dutse ka daka da shi ya tsage, kome girmansa.
- Ga takobi Shafau, kome ka sara da shi ya karye kome maridancin aljani, ya bi ka.

- Ga sanda, idan ka girgiza ta, qirarta kamar aradu ce, sai tartsatsin wuta ya riqa fita yana kashe mutane.

Mai karatu zai so ya ga cewa shin waxannan kayan yaqi sun taimaka wa babban tauraro ko kuma ba gaske ba ne, sai dai ba a xauki wani lokaci mai tsawo ba aka bayyana wa mai karatu cewa babban tauraro ya yi amfani da takobin nan shafau da kuma wannan kulki,kuma dukkansu sun taimake shi.Wannan ya sanya shi zama ba-xokin gaske na kusa a sakamakon yadda mai karatu ya zaqu don ganin abubuwan da aka lissafa masa a kan yiwuwarsu sun afku ko akasin haka. Wannan ba-xoki ne mai nuna yadda duk mutumin da yake da niyyar taimako a rayuwa shi ma za a taimake shi, kamar yadda hakan ya faru a kan babban tauraro.

Mai karatu zai so ganin ko abin da aka takalo masa za a cika shi ko kuwa, haka kuma zai xokanta da ganin yadda za ta kasance kamar haka :

> Ya tashi ya durqusa ya ce, "Na rantse da Allah da addinin da ka sani, ban santa ba, ba kuwa wanda ya san ta tsakanin mutum ko aljan. Yarinya ta tashi ta yi gaisuwa da kanta guna. Na ce mata, "Bari kuka, kya koma gida, in Allah ya so. Ni ma ina da nufin komawa Sakkwato, daga can har Kwantagora". Da ta ji haka sai ta ce, "Ai kuwa su

> ma 'yanuwammu ne bisa ga abin da na ke ji, duka asalimmu xaya da su". Na ce, " I, hakanan ne (*Ganxoki,* sh. 22).

Wannan ba-xoki ne na gaske na kusa, domin kuwa marubucin littafin ya yi qoqarin jawo hankalin mai karatu ne ta hanyar amfani da waxannan jumloli kamar haka:

- Na ce mata, "Bari kuka, kya koma gida, in Allah ya so.

- Ni ma ina da nufin komawa Sakkwato, daga can har Kwantagora.

Haqiqa wannan ba-xoki da marubucin littafin ya yi amfani da shi, sun samu ne ta hanyar amfani da jumloli da suka sanya mai karatu zaquwar son ganin abin da zai faru a gaba. Marubucin ya nuna yadda Sarkin yaqi Ganxoki ya yi alqawarin mayar da yarinyar nan gida wajen iyayenta. Sa'annan kuma ba a daxe ba aka ga ya mayar da ita gida. Wannan ne yake nuna mana cewa ba-xoki ne na gaske kuma na kusa. Wannan ba-xoki ne mai nuna muhimmancin cika alqawari kamar yadda aka nuna halayyar babban tauraro ta tausayi da kuma riqon amana.

### 4.3.2 Ba-xokin Gaske na Nesa

Ba- xokin gaske na nesa, dabara ce ta marubuta da suke ba wa mai karatu hasken faruwar wani abu, wanda mai karatu zai ta bin diddigin

ganin yadda za ta kasance, sai dai akan xauki tsawon lokaci ba tare da ganin afkuwar abin nan ba sai a nesa. Wannan ya sanya waxannan qagaggun labarai suka yi amfani da wannan dabara ta ba-xokin gaske na nesa,domin jawo hankalin mai karatu. Misali a cikin littafin *Jiki Magayi* an yi amfani da wannan dabara don jawo hankalin mai karatu a kan ci gaba da karanta wannan littafi. Wannan ne ya sanya aka yi amfani da ba-xokin gaske na nesa kamar haka :

> Da asalatun fari ya aika aka kira masa wani malamin qasa. Da ya zo ya ce yana so ya ba shi labari.Malamin ya share qasa ya buga, ya ce, "Na ga maganar aure da kuwa haihuwa tsakani, na ga wani kuma ya qwace gabanka, amma idan ka maida hankali za ka ture shi. Kuma na ga wahala cikin auren nan, in ka yi wata rana za ka yi da na sani. In ka bi shawarata kada ka saka yatsa cikin wannan al'amari, ka bar shi yadda Annabi ya bar duniya. Saura Allah ya sani" (*Jiki Magayi, sh.* 2).

Wannan ba-xokin gaske ne na nesa, dalili a nan shi ne, malamin da Malam Shaihu ya kirawo a kan mafarkin da ya yi ya shaida masa gaskiya cewa akwai maganar aure, sai dai yana ba shi shawara a kan ka da ya jefa kansa ciki, domin zai yi nadamar hakan a gaba. Wannan ba-xoki ne na gaske amma na nesa, domin mai karatu zai ga yadda Malam Shaihu yake nadamar aure da haihuwa. Wannan ba-xoki ne na gaske kuma na nesa.  Dalilan kasancewarsa na nesa shi ne, jimlar da

marubucin littafin ya yi amfani da ita ce ta haifar da wannan ba-xoki, Misali:

-Na ga maganar aure da kuwa haihuwa tsakani.

Waxannan jumloli su ne qashin bayan haifar da wannan ba-xoki, domin kuwa da zarar an cire su, za a ga cewa babu wani abu da zai jawo hankalin mai karatu. Haka kuma idan mai karatu ya ci gaba da bibiyar wannan labari zai ga yadda ta kasance, har aka yi wannan aure aka sami qaruwa, amma duk ba a kusa ba.

Mai karatu zai yi ta bin diddigin ganin ko alwashin nan da Abubakar ya ci na cewa duk daren daxewa sai ya rama abin da aka yi masa ko kuwa wani abin ne zai faru akasin haka. Misali inda aka ce :

> Ya ce mata, "Haba, iya idan ni xam mutum biyu ne, sai na rama. Zan shiga duniya, da ko wane hali na sani Allah zai taimake ni. Amma ka da ki damu. Ga Audu nan da qanwata da kakarmu, sun ishe ki zaman duniya, ni kuwa idan da rai wata rana za ki ga na komo (*Jiki Magayi*, sh. 9).

Waxannan jumloli da aka yi amfani da su, su ne suka haifar da wannan ba-xoki, misali:

- Haba, iya idan ni xam mutum biyu ne, sai na rama.
- Zan shiga duniya, da ko wane hali na sani Allah zai taimake ni.

- Ni kuwa idan da rai wata rana za ki ga na komo. Waxannan jumloli su ne suka taimaka wajen qulla zaren wannna dabara ta jawo hankalin mai karatu.

Sa'annan wannan alwashi da Abubakar ya ci na ramuwar abin da Zainabu ta yi masa ya tabbata. Mai karatu an sanya masa ba-xokin ganin yadda Abubakar zai rama, kuma tun daga lokacin mai karatu ke sanya ido domin ganin ramuwar ko kuma rashinta, sai dai marubucin ya tabbatar da ba-xokin a inda Abubakar ya rama bayan wasu lokuta. Wannan ne ya sanya shi zama ba-xokin gaske na nesa.

A nan wajen marubuci ya ba da hasken cewa abin nan da aka ce Abubakar ya samo, shi zai gaya masa inda zai samo shi, wanda mai karatu zai matsu sosai da ganin ta yadda Abubakar zai samo abin nan da aka ce masa ya samu, duk da akwai wahala a cikin nemansa. Ga misali kamar haka:

> Tausayinka- da sauqi ya ce, "Ina so ka samo mini qaron kalgo." Ya ce, "A ina zan sami wannan? Ban tava ganin wanda ya same shi ba." Ya ce, Ba shi a qasan nan, amma zan gaya maka inda idan ka tafi, ka samu (*Jiki Magayi*, sh.13).

Wannan ba-xokin gaske ne na nesa, dalilin kasantuwarsa hakan shi ne daxewa da wahalar da Abubakar ya sha kafin ya samu qaron Kalgo. Marubucin littafin ya tabbatar wa da mai karatu samuwar qaron Kalgo amma ba a kusa ba, don haka ne ya zama ba-xokin gaske na nesa. Haka kuma ba-xoki ne mai nuna yadda juriya a kan wani lamari take haifar da nasara, matuqar za a jure wahalhalun da za a iya fuskanta, kamar yadda hakan ya faru a kan Abubakar. Jumlolin da aka yi amfani da su ne, suka haifar da samuwar wannan ba-xoki. Jumlolin su ne kamar hakka:

-Tausayinka- da sauqi ya ce, "Ina so ka samo mini qaron kalgo."

-Ya ce, "A ina zan sami wannan? Ban tava ganin wanda -Ya ce, Ba shi a qasan nan, amma zan gaya maka inda idan ka tafi, ka samu. Waxannan su ne jumlolin da za su sanya mai karatu zumuxin ganin ko hakan zai faru a gaba.

A nan, mai karatu zai zaqu da ganin cewa ko Abubakar zai sami nasara ko kuwa, sai dai, da zarar ya ci gaba da karatun zai ga yadda za ta kasance. Misali kamar haka:

> Amma ka sani da wahala mai yawa a gabanka, ko rabin tafiyarka ma ba ka yi ba tukuna. Inda za ka

> samo abin nan, sai ka rabu da mutane, ka shiga can cikin Dawan Ruquqi, nan ne idan Allah ya yi maka katari, ya gajarta wahalarka, za ka samu. Amma fa, kai, samun abin nan sai namijin gaske! *(Jiki Magayi, sh.* 17).

Wannan ba-xoki ne na gaske kuma na nesa, saboda an takalo wa mai karatu batun irin wahalhalun da Abubakar zai fuskanta, an kuma shaida masa ko rabin tafiyarsa ma bai yi ba. Mai karatu zai gane wannan ba-xoki ne ta cikin sauqi, ta la'akari da jumlolin da aka yi amjfani da su kamar haka:

- Inda za ka samo abin nan, sai ka rabu da mutane.
- Ka shiga can cikin Dawan Ruquqi.
- Nan ne idan Allah ya yi maka katari, ya gajarta wahalarka, za ka samu.

A nan mai karatu zai so ganin wahalhalun da aka ambata wa Abubakar za su same shi ko kuma ba za su same shi ba, don haka da zarar mai karatu ya ci gaba zai ga Abubakar ya fuskanci wahalhalu da dama, amma wahalar ita ce ta cikin dawan Ruquqi inda ya yi karo da aljannu da yadda har sai da ya fitar da rai na samun wannan qaron kalgo. Don haka ba-xokin na gaske ne na nesa, haka kuma ba-xoki ne

mai nuna juriya a kan yadda wahalar rayuwa ke taimaka wa wajen samun nasara a dukkan lamarin da mutum ya sanya a gaba.

Marubucin wannan littafi ya yi amfani da ba-xokin gaske na nesa, wanda zai sa mai karatu son ganin ko burin samuwar wannan abu ga Abubakar mai yiwuwa ne ko kuwa dai wani abu ne zai faru, hakan ya sa mai karatu ci gaba da karatun don ganin me zai faru kamar haka:

> Dattijon ya ce, "Idan Allah ya gwada maka shi, za ka ga wurin da ya ke ya xauki haske sai ka ce rana. Shi kuwa xan qanqanen abu ne. Amma galibi idan ka je za ka xauka ya kan vace. Idan ka shiga Sanga ka sami batta, ka shafe ta da kitse, a ciki za ka saka in ka samu *(Jiki Magayi, sh.*19).

Wannan ba-xoki ne na gaske amma na nesa, domin marubucin littafin ya takalo wa mai karatu batun yadda Abubakar zai sami qaron kalgo da kuma yadda qaron kalgon nan yake yin siddabaru a yayin da aka je za a xauka. Wannan batu an kawo shi ne a shafi na (19) sai dai a shafi na (25) aka ga faruwar al'amarin. Don haka ba-xoki ne na gaske na nesa, dalilin da ya sanya ya zama ba-xokin gaske na nesa shi ne tun haxuwar Abubakar da wannan dattijo ya bayyana masa yadda zai ga qaron kalgo idan har ya yi katarin samunsa. Haka kuma dukkan yanayin da aka bayyana wa Abubakar na qaron kalgo haka ya kasance

domin hakan ya gani, sai dai sai da aka xauki tsawon lokaci kafin faruwar hakan. Jumlolin da aka yi amfani da su wajen haxa wannan ba-xoki su ne kamar haka:

- Dattijon ya ce, "Idan Allah ya gwada maka shi, za ka ga wurin da ya ke ya xauki haske sai ka ce rana.

Wannan jumla ita ce za ta sanya mai karatu cikin yanayi na son ganin ko abin zai faru ko akasin haka.

> Amma ka sani da wahala mai yawa a gabanka, ko rabin tafiyarka ma ba ka yi ba tukuna. Inda za ka samo abin nan, sai ka rabu da mutane, ka shiga can cikin Dawan Ruquqi, nan ne idan Allah ya yi maka katari, ya gajarta wahalarka, za ka samu. Amma fa, kai, samun abin nan sai namijin gaske! *(Jiki Magayi, sh.* 17).

Mai karatu cikin sauqi zai gane cewa ba-xokin na nesa ne, domin jumlar da marubuci ya yi amfani da ita, ita ce ke haska cewa samun qaron kalgon nan ba a kusa za a same shi ba. Waxannan jumloli su ne kamar haka:

- Amma ka sani da wahala mai yawa a gabanka.
- Ko rabin tafiyarka ma ba ka yi ba tukuna.

Wannan ba-xoki ne na gaske kuma na nesa, saboda an takalo wa mai karatu batun irin wahalhalun da Abubakar zai fuskanta, an kuma shaida masa ko rabin tafiyarsa ma bai yi ba. A nan mai karatu zai so ganin wahalhalun da aka ambata wa Abubakar za su same shi ko kuma ba za su same shi ba, don haka da zarar mai karatu ya ci gaba zai ga Abubakar ya fuskanci wahalhalu da dama, amma wahalar da ya fi fuskanta ita ce ta cikin dawan ruquqi inda ya yi karo da aljannu da yadda har sai da ya fitar da rai na samun wannan qaron kalgo. Don haka ba-xokin na gaske ne na nesa. Wannan ba-xoki ne mai nuna qarfin juriya da dagewa a kan neman wani abu.

Marubucin littafin ya yi qoqarin jawo hankalin mai karatu ta hanyar takalo masa da batun haihuwar Malam Shaihu, domin kuwa dalilin da ya sanya shi auren Zainabu shi ne, haihuwa. Wannan ne ya jefa mai karatu cikin son ganin yadda al'amari zai gudana, inda aka ce:

> Domin ba kwaxayi kaxai ne ya sa attajirin nan ya yi maka wannan abu ba. Dalili dai yana son xa ne, an kuwa gaya masa idan ya auri yarinyan nan zai samu. Sa'an nan Abubakar ya ce, “Ashe hakanan ne?” Ya ce, “I”. Abubakar ya ce, “To, zai kuwa samu?” Ya ce, “Lalle zai samu, domin wannan magana ba nufin mutum ba ce, ikon Allah ne *(Jiki Magayi,* sh.12- 13).

Wannan ba-xoki ne na nesa, kuma na gaske. Wanda a nan an tabbatar wa da Abubakar cewa Malam Shaihu zai samu xa da shi da Zainabu, kamar yadda a baya aka tabbatar wa da Malam Shaihu cewa idan ya auri Zainabu zai samu haihuwa. A nan marubucin wannan littafi ya daxa kawo wa mai karatu wannan batu ne wanda hakan zai daxa sanya ya janyo hankalinsa game da ci gaba da karanta littafin, don ganin an tabbatar masa da abin da aka baxokanta masa. Wannan ba-xoki ne mai nuna yadda dukkan wani abu da zai faru a rayuwa babu makawa zai faru da ikon Allah, kamar yadda aka ga haka a kan haihuwar Zainabu da Abubakar yake tambaya a kai, aka kuma tabbatar masa da cewa ikon Allah ne. Dukkan waxannan jumloli su ne marubucin ya haxa wajen sanya wannan ba-xoki na nesa ga mai karatu da kuma xokin ganin abubuwan da za su faru a gaba.

Har ila yau kuma, marubucin littafin *Idon Matambayi* ya yi amfani da ba-xokin gaske na nesa, wanda hakan ya taimaka masa wajen jawo hankalin mai karatu. Marubucin wannan littafi, ya yi amfani da jumloli ne wajen sanya wa mai karatu ba-xoki a cikin ransa. Daga cikin ba-xokin gaske na nesa da aka yi amfani da su a cikin wannan littafi akwai waxannan:

- Xauke kuwa ya zauna a gida sai azahar ta yi ya tafi Kafi,.
- Kuma a Kafi xin ya duba a hankali ko Allah ya sa ya ga wani gidan attajiri wanda za su kai wa hari da dare.

Mai karatu a nan zai so ganin yadda za a shirya wannan sata a gidan wannan attajiri, domin ba lallai ne abin da aka ambata masa ya zama ya faru ba, sai dai idan ya ci gaba da karanta litttafin zai ga yadda ta kasance kamar haka:

> Aka haxa shawara Qwace da Idon Matambayi su tafi hanyar da fatake masu wuchewa, su lave har Allah ya kawo rabonsu. Xauke kuwa ya zauna a gida sai azahar ta yi ya tafi Kafi, wani gari ne kusa da Sauke- mu raba, ya sayo abinchin da za su chi da dare, kuma a Kafi xin ya duba a hankali ko Allah ya sa ya ga wani gidan attajiri wanda za su kai wa hari da dare. Suka haxu a kan haka, shawara ta zauna *Idon Matambayi,* sh. 6).

A nan marubucin wannan littafi ya takalo wa mai karatu batun shawarar da varayin nan suka yi, saboda sun tsaya a kan yadda suke ganin za su tsara yadda za su gano wani gida da za su kai hari su yi sata. Mai karatu da ya ci gaba da karanta littafin nan zai ga cewa varayin nan tun a shafi na (6), suka shirya gano inda za su je su yi sata, amma hakan bai faru ba sai a shafi na (40). Don haka wannan ba-xoki ne na gaske na nesa.Haka kuma ba-xoki ne mai fito da halayyar

varayi ta yin juriya da yin dukkan wani shiri a kan cim ma burinsu na yin sata.

### 4.3.3 Ba-xokin Gangan

Wannan dabara ce da marubuta suke yin amfani da ita don jawo hankalin mai karatu ci gaba da karatun littattafansu. Sai dai ba kowanne marubuci ne yake son amfani da wannan ba-xoki na gangan ba, duk da cewa waxannan littattafai an samu sun yi amfani da shi a wasu wurare. Littafin *Jiki Magayi* ya yi amfani da wannan dabara ta ba-xokin gangan, wanda a nan, aka takalo wa da mai karatu faruwar yadda za ta kasance tsakanin iyayen Zainabu da Malam Shaihu, kamar yadda aka kawo shi a nan:

> Da gari ya waye Malam Shaihu ya aika aka kirawo masa Malam Sambo, ya faxa masa dukkan abin da suka yi da Zainabu. Sai Malam Sambo ya ce, " Tun da ya ke ka ba ta turaren shi ke nan, kada ka sake neman ganinta, su da kansu sa aiko a neme ka (*Jiki Magayi, sh.*9).

Wannan ba-xoki ne na gangan da marubucin wannan littafi ya yi amfani da shi, haka kuma, ta hanya mai sauqi mai karatu zai gane yadda aka haxa wannan ba-xoki na gangan kamar haka :

- Tun da ya ke ka ba ta turaren shi ke nan,.
- Kada ka sake neman ganinta, su da kansu sa aiko a neme ka.

Waxannan su ne jumlolin da marubucin wannan littafi na *Jiki Magayi* ya yi amfani da su wajen qulla wannan ba-xoki a cikin littafinsa.

A wannan labari,an nuna cewa shi Malam Sambo ya tabbatar wa da Malam Shaihu ba sai ya aika gidan su Zainabu ba, su da kansu za su neme shi. Wannan dai ba ta kasance ba, duk da cewa asirin nan ya kama Zainabu ta ji tana qaunar Malam Shaihu, amma mahaifinta bai aika wa Malam Shaihu ba. Hasali ma shi Malam Shaihu ne ya aika da batun auren zuwa ga mahaifin Zainabu wato Malam Audu, har ya tabbatar masa da cewa shi ba zai aura masa ba sai dai kotu. Wannan ya faru ne a shafi na (11).

Mai karatu dai, zai sanya idanu da kuma zaquwar ganin yadda xaya daga cikin qananan taurari ya ci alwashin shirya dabarar da za a yi wa Musa sata. Domin kuwa hakan ne zai ba da damar ci gaba da jawo hankalin mai karatu don ganin yadda za ta kasance kamar haka:

> Batsokana ya che," To,kun ga irin dabarar Da Qwache ya yi tana da kyau, kuma ina so kowa a chikinku ya yi irinta. Idan kuka yi haka ba na shakka zan iya fitad da dabarar sache kayan Musa duka.Duk karkarar nan ba mai dukiyar Musa. Idan Allah ya xora mu a kansa muka washe shi, dukammu mun sami dukiyar vatarwa har wani

lokachi mai tsawo, watakila ma daga nan kome ya ishe mu, mu bar sata *(Idon Matambayi*, sh.24).

Wannan ba-xoki ne na gangan da marubucin littafin ya yi amfani da shi don jawo hankalin mai karatu, a inda wannan ba-xoki ya bayyana shi ne, furucin da xaya daga cikin taurarin littafin ya yi. Wato Batsokana, inda ya ce:

- Batsokana ya che," To,kun ga irin dabarar Da Qwache ya yi tana da kyau.
- Kuma ina so kowa a chikinku ya yi irinta.
- Idan kuka yi haka ba na shakka zan iya fitad da dabarar sache kayan Musa duka.

Waxannan su ne jumlolin da suka haifar da ba-xoki a wannan waje, domin kuwa xaya daga cikin taurarin ya nuna cewa shi ne zai shirya ya kuma fitar da dabarar da za a yi wa Musa sata, sai dai idan mai karatu ya ci gaba da karatun wannan littafi zai ga cewa ita kanta satar da aka yi wa Musa babu Batsokana aka shiryata, duk kuwa da cewa da shi aka je gidan Musa a matsayin masu sayen goro. Mai karatu zai ga yadda marubucin ya karkatar da tunaninsa ta hanyar tsame Batsokana a cikin jerin waxanda suka yi sata a gidan Musa, wanda hakan kuma na da dalili na aiwatar da dabarun da marubuci ke son yin amfani da su don jawo hankalin mai karatu.

A nan kuwa, an yi amfani da ba-xokin gangan ne, domin shi ne mafi dacewa don xorewar ci gaban littafin. Wannan dabara ce ta marubuci don jawo hankalin mai karatu, saboda mai karatu zai so ganin yadda za ta kasance, inda aka ci gaba da labari kamar haka :

> Kafin mu kai wani aljani kuma ya ba uban labari cewa xansa ya musulunta. Sai ya yi fushi. Da zuwammu ya sa aka xaure xan, ya ce a tafi da ni wani ruwa wanda ya ke horo da shi a jefa. Sanyinsa ya fi qanqara. Sauran kamar sa'a xaya kafin a kai ga ruwan nan sai Allah ya nufi aljanin nan da gajiya, ya sauke ni don ya huta, sai barci ya share shi. Na sance kaina, na nemo babban dutse na kwantara wa aljanin a ka, kai ya ratsatstsake ya mutu (*Ganxoki,*sh. 40).

Wannan ba-xoki ne na gangan, marubucin ya yi amfani da wasu jumloli don cim ma manufarsa kamar haka:

- Da zuwammu ya sa aka xaure xan, ya ce a tafi da ni wani ruwa wanda ya ke horo da shi a jefa.

A na, mai karatu ya karanta cewa aljani Mazalzalu ya sa a je a jefa Sarkin yaqi Ganxoki cikin wani ruwa mai sanyi da yake horo da shi, bayan ya kama xansa wato Zalzalu ya xaure. Mai karatu dai ya ga inda aljanin da aka umarta ya je ya jefa Ganxoki cikin wannan ruwa

gajiya ta sa ya ajiye Ganxoki ya kwanta bacci. Sai ga shi Ganxoki ya kuvuta ta hanyar kashe aljanin nan. Wannan ke nuna wa mai karatu an jawo hankalinsa ne kawai, amma ba don a tabbatar da batun a gaske ba. Wannan ya zama ba-xokin gangan saboda niyyarsu ta su halaka Ganxoki da kuma yadda mai karatu ya ga an kama Ganxoki zai iya zaton cewa burinsu zai cika, kuma Ganxoki ba zai kuvuta ba, don haka kuvutar da Ganxoki ya yi ita ta haifar da aukuwar ba-xokin gangan.

A nan dai mai karatu an baxokanta masa son ganin umarnin da Sarki ya bayar na a zo da wani mutum gabansa ya faru, kuma idan har ya faru wanne sakamako aka samu. Wannan ne ya sanya ba da damar jawo hankalin mai karatu wajen ci gaba da qoqarin ganin yadda za ta kasance, inda aka kawo wannan batu kamar haka :

> Sarki ya ce, "Hakanan ne, Ganxoki. To, ina dabara? "Dabara tana gareka, kai ka san abin da ya kamata. Ni dai na faxakad da kai ne, domin kai ne wuqa kai ne nama." Ya ce, "A tafi a zo da shi (*Ganxoki,* sh. 11).

Wannan ba-xoki ne da marubuci ya yi amfani da shi don jawo hankalin mai karatu, haka kuma ya yi amfani da jumloli masu sauqi waxanda su ne suka haifar da wannan ba-xoki, Ga su kamar haka:

- Ya ce, "A tafi a zo da shi. Wannan jumla ita ce ta sanya karatu zaquwar son ganin yadda za ta kasance, musamman da aka ce a tafi a zo da Sarkin Gwari Barau. A nan za a ga cewa Sarki ya yi umarni ga Sarkin yaqi Ganxoki da a je a zo masa da Sarkin Gwari Barau, don haka mai karatu a nan zai ci gaba da karatun littafin da zumuxin ganin an je an zo da Sarkin Gwari Barau, kamar yadda Sarki ya umarci Sarkin yaqi Ganxoki. Amma sai ga shi ba a zo da shi ba, Ganxoki ya murxe masa kai, har aka ga cewa Sarkin ya faxakar da cewa shi bai ce a aikata hakan ba, ya so dai a zo masa da shi ne, amma ya san aikin Sarkin yaqi Ganxoki ne. Wannan haqiqa ba-xoki ne na gangan, domin mai karatu ya karanta cewa za a je a zo da Sarkin Gwari Barau, amma sai ga shi ba a zo da shi ba.

Mai karatu zai so ganin cewa ta yaya za a kawo kan wannan mutumi da kowa yake tsoro, hakan ne zai sa ya ci gaba da karanta littafin, an kawo ba-xokin kamar haka:

> Ya ce, "Wannan magana ba shakka Waziri, haka za ta gudana. To, ina dabara? "Ce ka ba shi ita, amma sadakinta ba ka son dukiya, sai ya kawo maka kan Durungu Hambama. Ya tafi can ya canye shi, kowa ya huta. Amma xan taqadarin yaron nan nasa kada ka bari su je tare. Kul suka haxu, na tabbata mutum ko aljan, babu mai iya ja da su (*Ganxoki,* sh. 18).

Wannan ba-xoki ne na gangan da aka yi amfani da shi a cikin wannan littafi, domin kuwa marubucin wannan littafi ya nuna cewa, ga 'yar Sarkin da Ganxoki yake so, an yi shawara da Waziri a kan cewar za a ba shi auren 'yar Sarkin bisa sharaxin sadakinta shi ne kan Durungu Hambama. Dalilin hakan kuwa saboda suna ganin tun da al'adar shi Durungu Hambama ne cinye mutum sai ya cinye Ganxoki a huta. Sai dai kuma ba a ga inda shi Ganxoki ya kawo kan Durungun ba, haka nan su ma ba su sami labarin cewa Durungun ya cinye Ganxoki ba. A qarshe ma dai shi Durungu Hambaman ne ya miqa wuya ga Sarkin yaqi Ganxoki. Saboda haka wannan ya zama ba-xokin gangan, wato kawo kan Durungu a matsayin sadaqin auren ‘yar Sarki. Wannan ya kasance ba-xoki ne mai nuna dabarar yaqi ta qarqashin qasa, domin kuwa dai an tura Ganxoki ne bisa shirya masa zagon qasa don ya halaka, sai ga shi hakan bai kasance ba. Marubucin ya yi amfani da dukkan jumlolin ne wajen haxa wannan ba-xoki. An qulla zaren dabarar jan hankalin mai karatu ta hanyar son ganin ko za a sami nasara a kan Ganxoki a kashe shi, ko kuma akwai mafita, da zarar mai karatu ya ci gaba da karatu zai ga yadda ta kasance kamar yadda aka kawo shi a nan:

> Shi kuwa Sarkin nan yana da gunki. Akwai wani aljani, dukan abin da ya ke so sai ya tambayi gunkinsa labarin duniya, ya ba shi labarina duka. Da zuwansu Sarki ya ce a kashe ni, amma Waziri ya ce a bar ni sai gobe a qona ni a tsakar jama'a kowa ya gani. Tun cikin dare aka hura wuta ganga ganga. Aka kai ni cikin xakin gunki aka qulle kafin gari ya waye. Na ga yau ga ni xaki xaya da gunki. Sai na kama zikiri da salati. Aljanin cikin zuciyarsa ta yi sanyi da ya ji ina ambaton Allah. Ya fito ya ce, "Samari, ba ka musuluntad da ni ba?" Sai na musuluntad da shi. Shi kuwa xan wani aljani ne sunansa Zalzalu xam Mazalzalu. Kafin gari ya waye ya sace ni, ya tashi da ni ya nufi garin ubansa (*Ganxoki,*sh. 40).

Wannan ba-xoki ne na gangan, saboda mai karatu zai ga cewa tattaunawar da mutanen da suka kama Sarkin yaqi Ganxoki suka yi a kan cewa ka da su kashe shi, su kai wa Sarkinsu, shi kuma ya nuna lallai a kashe Ganxoki, sai Waziri ya ba da shawarar a bari sai gobe a tsakiyar taron jama'a a qone Ganxoki. A nan ne ma har aka ga yadda aka haxa wuta tun dare da kuma yadda aka shigar da Ganxoki xakin da gunki yake, haka kuma an ga yadda Ganxoki ya kuvuta daga wannan tanadi na qona shi da aka yi ta hannun aljanin da ke cikin gunkin mutanen nan. Wannan ne ya qara tabbatar mana da cewa ba-xokin na gangan ne, domin dai Ganxoki ya kuvuta daga shirin qona shi da aka yi. Wannan dabara ce da marubucin ya yi amfani da ita don

jawo hankalin mai karatu. An yi amfani ne da jumloli waxanda suka haifar da faruwar wannan ba-xoki, Ga su kamar haka :

- Da zuwansu Sarki ya ce a kashe ni.
- Amma Waziri ya ce a bar ni sai gobe a qona ni a tsakar jama'a kowa ya gani.

Haqiqa mai karatu zai damu matuqa da son ganin yadda Ganxoki zai sami kuvuta daga halin da ya sami kansa a ciki, ga dai yadda al'amarin ya gudana kamar haka:

> Kafin mu kai wani aljani kuma ya ba uban labari cewa xansa ya musulunta. Sai ya yi fushi. Da zuwammu ya sa aka xaure xan, ya ce a tafi da ni wani ruwa wanda ya ke horo da shi a jefa. Sanyinsa ya fi qanqara. Sauran kamar sa'a xaya kafin a kai ga ruwan nan sai Allah ya nufi aljanin nan da gajiya, ya sauke ni don ya huta, sai barci ya share shi. Na sance kaina, na nemo babban dutse na kwantara wa aljanin a ka, kai ya ratsatstsake ya mutu (*Ganxoki,* sh. 40).

Wannan ba-xoki ne na gangan, domin kuwa aljani Mazalzalu ya sa a je a jefa Sarkin yaqi Ganxoki cikin wani ruwa mai sanyi da yake horo da shi, bayan ya kama xansa wato Zalzalu ya xaure. Mai karatu dai ya ga inda aljanin da aka umarta ya je ya jefa Ganxoki cikin wannan ruwa gajiya ta sa ya ajiye Ganxoki ya kwanta bacci. Ba da jimawa ba sai ga shi Ganxoki ya kuvuta ta hanyar kashe aljanin nan. Wannan ke

nuna wa mai karatu an jawo hankalinsa ne kawai, amma ba don a tabbatar da batun a gaske ba. Wannan ya zama ba-xokin gangan saboda niyyarsu ta su halaka Ganxoki da kuma yadda mai karatu ya ga an kama Ganxoki zai iya zaton cewa burinsu zai cika, kuma Ganxoki ba zai kuvuta ba, don haka kuvutar da Ganxoki ya yi ita ta haifar da aukuwar ba-xokin gangan. Marubucin wannan littafi ya yi amfani da wannan dabara don jawo hankalin mai karatu, dangane da haka ya kawo ba-xoki kamar haka:

> Ya ce, "Wannan magana ba shakka Waziri, haka za ta gudana. To, ina dabara? "Ce ka ba shi ita, amma sadakinta ba ka son dukiya, sai ya kawo maka kan Durungu Hambama. Ya tafi can ya canye shi, kowa ya huta. Amma xan taqadarin yaron nan nasa kada ka bari su je tare. Kul suka haxu, na tabbata mutum ko aljan, babu mai iya ja da su" (*Ganxoki,* sh.18).

Wannan ba-xoki ne na gangan da aka yi amfani da shi a cikin wannan littafi. A nan, za mu fahimci cewa, jumlolin da aka yi amfani da sum su ne suka samar da wannan ba-xoki da mai karatu zai damu a kan sanin yadda al'amari ya kasance. Jumlolin su ne kamar haka:

-Ya ce, "Wannan magana ba shakka Waziri, haka za ta gudana.

- To, ina dabara? "Ce ka ba shi ita.
- Amma sadakinta ba ka son dukiya.
- Sai ya kawo maka kan Durungu Hambama.

Marubucin wannan littafi ya nuna cewa, ga 'yar Sarkin da Ganxoki yake so, an yi shawara da Waziri a kan cewar za a ba shi auren 'yar Sarkin bisa sharaxin sadakinta shi ne kan Durungu Hambama. Domin suna ganin tun da al'adar shi Durungu Hambama ne cinye mutum sai ya cinye Ganxoki a huta. Sai dai kuma ba a ga inda shi Ganxoki ya kawo kan Durungun ba, haka nan su ma ba su sami labarin cewa Durungun ya cinye Ganxoki ba. A qarshe ma dai shi Durungu Hambaman ne ya miqa wuya ga Sarkin yaqi Ganxoki. Saboda haka wannan ya zama ba-xokin gangan, dalilin da ya sanya ya zama ba-xokin gangan kuwa shi ne rashin kawo kan Durungu Hambama a matsayin sadakin auren da aka nema daga wajen Ganxoki.

### 4.4 Tarken Matanonin Xarsau a Littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Msatambayi* da *Ganxoki*

A qoqarin marubuta waxannan littattafai don samun damar riqe tunanin mai karatu don jawo hankalinsa sun yi amfani da xarsau daban-daban a cikin littattafansu. Sai dai kowanne marubuci akwai

dabarar xarsau da ya fi yin amfani da ita da ta taimaka masa wajen isar da saqon littafinsa. Marubuta waxannan qagaggun labarai, sun yi amfani ne da jumloli waxanda suke sanya xarsau a zuciyar mai karatu. Haqiqa dukkan xarsau da suka yi amfani da su za a fahimci cewa suna amfani ne da jumloli masu haifar da waxannan dabaru na xarsau a cikin littattafansu.

### 4.4.1 Xarsau na ban Tausayi

A wannan gava, mai karatu an xarsa masa tausayi ne dangane da haska masa irin rayuwar da Kyauta ya sami kansa a sakamakon asirin da aka yi masa, kamar yadda marubucin ya kawo xarsau xin tausayin kamar haka:

> Da gari ya waye Kyauta ya tashi. Bayan ya wanke ido ya yi salla ya shiga ya gaida ubansa da uwa tasa, ta ba shi karin kumallo, ya ce za shi makaranta. Ya fita sai xakin ubansa,ya iske kuxi a zube a buzu, uban kuwa ya fita qofar gida. Sai ya sa hannu ya xebi sule biyu ya fita abinsa. Maimakon ya tafi makaranta sai ya guje wa abokan zuwansa ya shiga gari, ya kashe kuxinsa (*Jiki Magayi,* sh. 30)

Mai karatu zai fahimci xarsau ne na ban tausayi ta hanyar jumlolin da aka yi amfani da su a wannan labari. Dukkannin jumlolin suna bayyana xarsau ne na ban tausayi kai tsaye.Mai karatu ya karanta a

baya ya ga irin halayya da xabi'u na kirki da Kyauta ya ke da su, kuma ya karanta cewa Abubakar ya haxa magani don lalacewar xan Zainabu. Haka kuma mai karatu ya fara ganin tasirin maganin da Abubakar ya yi, domin tun da Kyauta yake bai tava shiga xakin mahaifinsa ya xauki abu ba. Amma lokaci xaya sai ga shi a sanadiyyar asirin da Abubakar ya yi masa na neman jefa shi cikin mummunar hanya ya fara tasiri a kansa. Marubucin wannan littafi baya ga xarsau na ban tausayi da ya xarsa shi a zuciyar mai karatu a kan yaron nan Kyauta xan Malam Shaihu, ya sake yin amfani da damar xarsa wa mai karatu xarsau na ban takaici a kan abin da Abubakar ya yi na yin asirin da zai lalata Kyauta. Wannan xarsau ne na ban tausayi kan cewa maganin Abubakar ya fara tasiri a kan Kyauta, yaro mai kirki abin farin cikin mahaifinsa, haka kuma xarsau na takaici ne ga halayyar Abubakar ta xaukar fansa a kan Kyauta. A nan mai karatu, zai samu xarsuwar tausayin mahaifiyar Abubakar, da zarar ya ci gaba da karanta labarin inda marubucin ke qoqarin xarsa wa mai karatu xarsau na ban tausayi kamar haka :

> Da ya koma gida ya faxa wa uwa tasa abin da ya ke tsakaninsa da Zainabu. Uwar ta ce, "Ai ni ko da na sani ba za ka auri Zainabu ba, domin kuwa tana da masoya masu arziqi, ka sani kuwa kome na duniyan nan ba duka a ke yi domin Allah ba,

> sai don dukiya. Haqura, ka nemi daidai da kai" (*Jiki Magayi,* sh. 9).

Wannan haqiqa xarsau ne na ban tausayi. Haqiqa dukkan jumlolin da aka yi amfani da su, suna xauke ne da xarsau na ban tausayi, domin kuwa mahaifiyar Abubakar ta ji zafin abin da aka yi masa, amma sai ta yi dauriya ta kuma yi masa nasiha da nuna masa halin rayuwa a wannan zamani matuqar aka ce mutum ba shi da kuxi. Haqiqa akwai akwai xarsau na ban tausayi dangane da yadda mahaifiyar Abubakar take yin wannan nasiha, abin da ya sanya wannan xarsau a zuciyar mai karatu shi ne furucin da mahaifiyar Abubakar ta yi a matsayin nasiha ga Abubakar. Haka kuma a xaya vangaren kuma xarsau ne na ban takaici a kan babban tauraro, saboda yadda ya qi yarda da qaddara ya zauna ya sami wata ya aura ya kyautata wa mahaifiyarsa. Marubucin wannan littafi ya yi qoqarin xarsa wa mai karatu tausayi a zuciyarsa dangane da nuna masa irin matsanancin halin da Malam Shaihu ya sami kansa a kan rashin haihuwa, duk kuwa da cewa komai na daxin zaman duniya yana da shi, sai dai rashin magaji. Wannan ne zai sanya mai karatu jin tausayin Malam Shaihu, inda marubucin ya ci gaba da cewa:

> Shekararsa ashirin da yin aure, amma bai tava haihuwa ba. Ya yi aure da yawa.

> Kullum gidansa ba a rasa matan aure huxu. Ya vatad da dukiya ba iyaka wajen malamai da bokaye da ‘yam bori garin neman maganin haihuwa, amma cikin matansa babu wadda ta tava ko vatan wata. Ko yaushe idan ya tuna da wannan babbar hasara ta rashin xa sai ransa ya dugunzuma, ya dami dukan mutanen gidansa da faxe-faxe, wani lokaci ma ba mai ganinsa a waje tun safe har wajen la’asar, yana can cikin xakinsa yana roqon Allah ya biya bukatarsa. Ko yaushe addu’arsa xaya ce, “Ya Ubangiji ka jiqaina ka ba ni xa ko da wane iri!” (*Jiki Magayi,* sh. 2).

Dangane da wannan al’amari na haihuwa musamman ga mutumin da yake da dukiya yake son ya sami magaji, rashin haihuwa a wajensa abu ne mai tausayi. A wannan gava marubucin wannan littafi ya fara da xarsau ne na ban tausayi ga Malam Shaihu a kan rashin haihuwa da bai yi ba, da kuma irin kullum addu’ar da yake yi a kan ya sami qaruwa. Marubucin littafin ya yi amfani ne da jumloli da suke nuna xarsau na ban tausayi kamar haka:

- Shekararsa ashirin da yin aure.
- Amma bai tava haihuwa ba.
- Ya yi aure da yawa.
- Kullum gidansa ba a rasa matan aure huxu.
- Ya vatad da dukiya ba iyaka wajen malamai da bokaye da ‘yam bori garin neman maganin haihuwa, amma cikin matansa babu

> wadda ta tava ko vatan wata.Haqiqa mai karatu zai fahimci xarsau ne na ban tausayi ta hanyar yadda marubucin ya haxa waxannan jumlololi masu xauke da xarsau na ban tausayi.

Wannan xarsau ne da aka buxe labarin da shi, sai dai ba da shi aka ci gaba da amfani ba don jawo hankalin mai karatu da xarsa masa xarsau daban-daban a cikin littafin ba. Mai karatu zai cika da tausayin Kyauta xan Malam Shaihu, domin ganin irin nadamar da ya yi a kan abin da ya aikata, kuma mai karatu yana da masaniyar cewa ba yin kansa ba ne, marubucin ya ci gaba da kawo labarin kamar haka:

> Sa'an nan ya ce a tara masa dukan malaman garinsu su yi wa ubansa addu'a. Aka taru tinjim a qofar gidan ubansa, ya fito da kaya ya yi ta raba musu har ya gama. Suka yi addu'a Allah ya jiqan Malam Usman. Kowa ya watse. Kashegari ya ce a tara masa musakai duka. Da suka gama taruwa ya fitad da dukan abin da ya rage cikin gidan ubansa,ya yi ta ba su, har kuxi suka qare ya shiga rabon tufafi, da tarkace da dabbobi. Saboda yawan dukiya duk garin babu wanda bai samu ba. Ya rabad da kayan sarai, ko allura bai xauka ba. Da ya gama ya tafi ya sallami Sarki. Duk gari suna ta mamaki, ba su tava ganin wanda ya yi haka ba. Ya sa uwa tasa a gaba, suka tafi har suka kai Galma. Ya sa ta a gidan ubansa. Ya shaida wa Sarki. Aka gama sha'anin gado, duk ya danqa wa uwa tasa, ya ce, "Ki yi abin da ki

> ka ga dama da shi. Ni zan tafi neman abin da zan rage alhakin nan da na xauka, ko Allah ya yi mini jinqai." Sai ya fita , daga shi sai sandarsa, da gafaka tasa, da 'yar buta" *(Jiki Magayi,* sh. 51).

Wannan xarsau ne na ban tausayi matuqa, domin Kyauta ya dawo hayyacinsa, sai dai mai karatu da kansa musamman da ya fahimci irin nadamar da Kyauta ya nuna har ya qi xaukar komai na daga dukiyar mahaifinsa da kuma tafiya don neman aiwatar da ayyuka nagari da yake da niyya don su zamar masa hanyar samun gafara, lallai akwai abin tausayi a ciki. Wannan shi ne xarsau xin da marubucin wannan littafi ya kammala da shi, kuma ba shi ne ya ci gaba da kawo wa ga mai karatu ba, haka kuma a farkon littafinsa da irin wannan xarsau na ban tausayi ya fara. A wannan littafi na *Jiki Magayi* za a iya cewa dabarar xarsau na ban takaici ita ce mafi dacewa wajen jawo hankalin mai karatu, domin za a ga cewa abubuwan da babban tauraro ya dinga aiwatarwa na ban takaici ne suka sanya har qaramin tauraro mai muhimmanci wato Kyauta ya lalace a sakamakon asirin da babban tauraron cikin wannan littafi ya yi masa.

A cikin littafin *Idon Matambayi* kuwa, an yi amfani da xarsau na ban tausayi, wanda suke nuna yadda marubucin littafin ya yi qoqarin jawo

hankalin mai karatu. A nan, marubucin littafin ya fara kawo wa mai karatu xarsau na ban tausayi ne a kan yadda su Idon Matambayi suke nuna rashin kyautawa ga matafiya da tare hanya da aikata qwacen dukiyar da ba su san yadda aka same ta ba. Marubucin littafin ya ci gaba da kawo labari mai xauke da xarsau na ban tausayi kamar haka :

> Mutane duk suka yi shiru, kowa jikinsa yana rawa, sai wani matsorachi a chikinsu ya che," Mun ji. To, nawa za mu ba ka?" Yayin da duk ake wannan abu Qwache yana lave yana jin abin da suke yi. Su kuwa ba su san yana nan ba. Idon Matambayi ya che, "Duk kayan jakunanku za ku sauke ku tafi". Suka che "To". Suka yi ta sauke kaya, kowa yana kora jakinsa yana tafiyarsa (*Idon Matambayi,* sh. 8).

Wannan xarsau ne na ban tausayi, marubucin littafinn ya haxa wannan xarsau ne ta hanyar amfani da jumloli da za su sa mai karatu fahimtar cewa xarsau ne na ban tausayi. Jumlolin da aka yi amfani da su a nan, su ne kamar haka:

- Mutane duk suka yi shiru.
- Kowa jikinsa yana rawa.
- Sai wani matsorachi a chikinsu ya che," Mun ji. To, nawa za mu ba ka?"

- Idon Matambayi ya che, "Duk kayan jakunanku za ku sauke ku tafi".

Suka che "To". Suka yi ta sauke kaya, kowa yana kora jakinsa yana tafiyarsa.

Waxannan su ne jumlolin da suka taimaka wa marubucin wannan littafi, wajen xarsa wa mai karatu xarsau na tausayin waxanda aka yi wa qwace.A nan, za mu ga cewa su dai varayin nan ba su san ta yadda waxannan mutane suka tara dukiyarsu ba. Sa'annan ga shi sun yi wo tafiya, ba su san takamaimai ma daga ina suke ba, amma ga su Idon Matambayi sun dage a kan sai sun ajiye dukkan kayansu sun tafi. Abin da ya haifar da wannan xarsau na ban tausayi ga mai karatu shi ne, yadda marubucin littafin ya nuna rashin imanin varayin nan da suka tare waxannan matafiya, hasali ma mai karatu baya ga jin tausayi na waxannan mutane zai sake jin xarsau na ban takaici a kan halayyar da varayin nan suka nuna ga waxannan matafiya. Wannan ke nuna cewa akwai xarsau na tausayi na matafiya da jin takaicin mummunar halayyar varayi duk a lokaci xaya, wannan dabara ce da marubucin ya yi amfani da ita don ya jawo hankalin mai karatu ya ci gaba da karanta wannan littafi, domin abu ne mai yiwuwa da mai karatu zai sanya a

ransa cewa duk waxannan munanan ayyuka da su Idon Matambayi suke aikatawa a gaba za su girbi abin da suka shuka.Marubucin wannan littafi ya xarsa wa mai karatu xarsau na ban tausayi ta hanyar nuna masa halin da mutanen Ganxoki suka sami kansu a ciki na qishirwa da yunwa, kamar yadda marubucin ya ci gaba da kawo xarsau xin kamar haka:

> Idan qishin ruwa ya dame su sai Garba ya ba su su kukkurva don su jiqa maqoshinsu. Idan ruwan ya qare, kafin a sami wani. Garba sai ya xebo musu lingavun ganyen kalgo suna taunawa, don su sami miyaun haxewa. Sai ka ga mace ta naxe qafafunta da kallabinta, shi ne kamar takalmi. Wata ta faxi tana buxe baski za ta mutu don qishirwa da yunwa, ita kwance, xanta kwance. Waxansu mazaje sun rabu da iyalinsu, ba su san inda suke ba. Allah ya tsari dukan Musulmi da fitina, da tashin hankali, duniya da lahira, amin! (*Ganxoki,* sh.10).

Wannan xarsau ne na ban tausayi, domin mai karatu an xarsa masa tausayin yadda wasu mata da qananan yara suke cikin tsananin wahala da yunwa da qishirwa. An xarsa masa hakan ne ta hanyar amfani da jumloli masu xauke da tausayi. Marubucin ya ci gaba da nuna wa mai karatu irin halin da waxannan mutane suka shiga a sakamakon

yaqi,wanda har ta kai suna tauna ganye kafin a samu ruwa. Sai dai a baya kaxan mai karatu an xarsa masa xarsau na ban tsoro, sai kuma ga shi ba a daxe ba an xarsa masa na tausayi, wato ke nan marubucin kan yi amfani da damarsa wajen shirya dabarun xarsau mabambanta don jawo hankalin mai karatu.Mai karatu zai ji an xarsa masa tausayi a zuciyarsa ne ta hanyar tausaya wa wasu mayaqa da aka kashe bayan sun dawo daga yaqi, inda marubucin yake cewa:

> Da gari ya waye mazaje suka yi karo, sai ka ce yankin dutse ke gamuwa, suka ja da baya suka gwabza, mutanen Inkwai suka yi xai xai, rabinsu duk sun kai takarda. Waxanda suka koma suka ba Sarkinsu labari. Ya ce "Mutuwa kuka gudo wa, ita kuka tarar." Ya sa duk aka kashe su. Ya ce, "Gobe wani kuma ya gudu ya ce zai kai labari!" (*Ganxoki,* sh. 27).

Wannnan xarsau ne na ban tausayi, domin kuwa sun gudu don ceton rai, sa'annan sun zo inda suke ganin za su tsira, amma an kashe su. Mai karatu zai fahimci wannan xarsau ne ta hanyar jumlolin da aka yi amfani da su wajen xarsa masa tausayi.Wannan dabara ce da marubucin wannan littafi ya yi amfani da ita don jawo hankalin mai karatu da xarsa masa tausayi a cikin ransa, haka kuma abin da ya xarsa wannan tausayi a zuciyar mai karatu shi ne kisan nan da aka yi

wa waxannan mayaqa da suka ga za a kashe su, suka dawo aka kuma kashe su a inda suke tsammanin samun tsira da mafaka.

### 4.4.2 Xarsau na ban Dariya

Haqiqa mai karatu zai sami xarsau na ban dariya a kan ganin yadda varayin nan suka gamu da gamonsu domin sun taro wanda ya fi su. Marubucin wannan littafin ya yi qoqarin xarsa wa mai karatu xarsau na ban dariya kamar haka:

> Da jin haka sai Qwache ya zaro wuqa zai dava wa mutumin sai hannunsa ya sage. Xauke kuma ya rugo da gudu ya kama shi da kokuwa, sai jikin mutumin ya riqa bin Xauke kamar wanda yake jan alewa. Idon Matambayi ya kai masa irin qullin nan nasa a chiki, sai hannunsa ya dafe. A'a Mutumin nan dai yana kallon qoqarin kowa a banza. Ya tambaye su ya che, " In che ko yanzu kun san ku ba kowan kowa ba ne?" "I, mun sani, kowa da wanda ya fi shi" (*Idon Matambayi,* sh. 20).

Wannan xarsau ne na ban dariya, domin marubucin wannan littafi ya yi qoqarin jawo hankalin mai karatu ta hanyar xarsa masa xarsau na ban dariya a wannan labari. Za a iya cewa kusan dukkan jumlolin nan suna xauke ne da xarsau na ban dariya,domin kuwa an nuna yadda su

Idon Matambayi suke yunqurin dukan mutumin da suka haxu da shi, amma da kansu suka haqura suka tabbatar da cewa duk abinka akwai wanda ya fi ka,nan da nan suka sallama. Marubucin littafin ya xarsa wa mai karatu xarsau na ban dariya ta hanyar bayyana masa yadda xaya daga cikin varayin nan ya sami kansa da kuma dabarar da ya yi ta zama makaho, inda yake cewa:

> Ya kama hanya yana tafiya chikin lokoki, bai aune ba sai yana kan titi. Ya bi titin kaxan, sai chan ya hango wani mutum yana tafe baqi qirin, ashe Xangadi ne. Allah ya sa xangadin bai gan shi ba, sai ya duba dama da shi sai ya ga wata 'yarhanya, ya bi ta ya bar titin, don kada ya gamu da Xangadin da ya hango. Ashe hanyar da ya bi chikin gida ta shiga, yana chikin binta sai ya yi aune yana chikin gida tsundun! Ga mutum biyu suna zaune a kan daven qofar wani xaki suna hira. Qwache ya rasa yadda zai yi, sai wata dabara ta zo masa. Ya rufe idanunsa kamar makafo, ya che da su "Allah zi wahidun, bayin Allah. ko kun chi kun rage ku bai wa makafo!" Lokachin da yake faxar maganan nan duk ya sake murya tasa ta zama kamar ta almajiri" (*Idon Matambayi,* sh. 23).

Wannan xarsau ne na ban dariya, domin marubucin littafin ya yi qoqarin jawo hankalin mai karatu ta hanyar xarsa masa xarsau na ban

dariya a wannan shafi. Domin ga Qwace nan ya shiga gidan mutane bai sani ba, saboda tsabar sanya zuciyarsa a kan sata. Sa 'annan mai karatu zai ga yadda a lokaci xaya Qwace ya ba shi dariya, domin har muryarsa ma ya sauya ta koma irin ta almajirai don tsoron ka da waxanda ya shigo wa gida su kama shi.Marubucin ya xarsa wa mai karatu xarsau na ban dariya ne dangane da nuna halayyar wani qaramin tauraro, domin kuwa yana rayuwa ne ta rashin sanin kansa, inda marubucin littafin ya ci gaba da cewa:

> Ban ga wanda hankalinsa bai tashi ba, sai wani mahaukaci wanda a ke ce masa Kwasau Sarkin yaqi. Sai ka ga yana gudu yana zamiya, kamar ya hau doki. Ya yi xamara cunkus da tsummoki. Ya rataya goruna da dagage, bai kula da abin da ake ciki ba. Yana cewa, "Bagazam Bagazam, dawa maganin dawo, dawo, maganin dawa!" *Ganxoki,* sh. 9-10).

Wannan xarsau ne na ban dariya da aka yi amfani da shi a wannan littafi, domin an siffanta yadda Kwasau Sarkin yaqi yake yin zamiya kamar wanda ya hau doki, sa' annan kuma yana tafe yana sambatu ga tsummokara a jikinsa. Wannan xarsau ne mai nuna yanayin mutumin da ba shi da hankali bai san ciwon kansa ba.An bayyana wa mai karatu yadda siffar wani aljani ta sanya wani daga cikin qananan

taurari cikin mawuyacin hali har ta kai da ya tsorata sosai, kamar yadda marubucin ya kawo labarin, inda yake cewa:

> Ya ta da kai zai dube su, sai suka fito masa da surarsu sosai, haqora zagozago. Nan da nan ya cika wando da zawo, ya bi dole, ba ko gardama (*Ganxoki,* sh. 38).

Wannan xarsau ne na ban dariya da marubucin ya yi amfani da shi don jawo hankalin mai karatu, domin kuwa ga yadda a lokaci xaya aka nuna yadda Sarki mai cikakken iko saboda ya ga aljannu a siffarsu ya tsorata ya kama zawo. Lallai akwai xarsau da zai sanya mai karatu dariya sosai.

**4.4.3 Xarsau na ban Takaici**

Marubucin wannan littafi, ya yi qoqarin xarsa wa mai karatu xarsau na ban takaici ne ta hanyar kawo masa irin yadda Abubakar ya qeqasa qasa a kan qin bin shawarar mahaifiyarsa da kuma qudurinsa na barin mahaifiyarsa da 'yan 'uwansa a kan neman fansa. Haka dai marubucin ya ci gaba da cewa kamar haka:

> Ya ce mata, " Haba, iya idan ni xam mutum biyu ne, sai na rama. Zan shiga duniya, da ko wane hali na sani Allah zai taimake ni. Amma kada ki damu. Ga Audu nan da qanwata da kakarmu, sun ishe ki zaman duniya, ni kuwa idan da rai wata rana za ki ga na komo *(Jiki Magayi,* sh.9).

Wannan xarsau ne na ban takaici da marubucin wannan littafi ya xarsa shi ga mai karatu. Don kuwa mai karatu ya ga dai abin da ya faru ga Abubakar, kuma mahaifiyarsa ta yi masa nasiha, ta ce ya sami wata daidai da shi. Sai dai sam, Abubakar bai yi na'am da abin da mahaifiyarsa ta gaya masa ba. Mai karatu zai ji an xarsa masa takaicin alwashin da Abubakar ya xauka har kuma da niyyar ya bar gida. Haka kuma bai damu ba zai dawo ya tarar da mahaifiyarsa da rai ko kuma ba zai dawo ya tarar da ita ba. Haka dai marubucin littafin ya yi amfani da wannan dama ya xarsa wa mai karatu xarsau na ban tausayin mahaifiyar Abubakar domin ga xan da ta haifa yana gaya mata cewa zai bar ta ya shiga duniya ga qannensa nan sun isheta rayuwa. Mai karatu zai ji an xarsa masa ban takaici a sakamakon yadda marubucin ya qulla dabarar jan hankalinsa, domin kuwa an nuna yadda asirin da Malam Shaihu ya yi wa Zainabu ya kama ta, don ga shi tana son a sauya maganar aurensu da Abubakar. Takaicin da mai karatu zai ji a ransa bai wuce na yadda mahaifin Zainabu zai shiga tsaka mai wuya ba, duk kuwa da cewa shi dattijo ne mai magana xaya, ga dai yadda ta kasance kamar haka:

> Da uwar Zainabu ta ji kukan da 'yarta ta ke
> yi sa'ad da a ke dukanta sai ta leqo ta ce, "
> Me ya faru da zafi haka? Kana so ka kashe

> ta ne?" Malam Audu ya ce mata, “A kan maganar aurensu ne da Abubakar. Kin sani dai ba shi yiwuwa a ce na amsa zam ba shi auren Zainabu, sa'an nan ta zo yanzu ta xauko mini wani wai shi Malam Shaihu, ta ce shi ta ke so da aure. Idan na bi maganarta kin sani na ji kunya ke nan, nan gaba babu wanda zai sake mai da ni dattijo, kowa sai ya yi ta yi da ni, a ce sabili da kuxinsa ne ya sa na fi son 'yata ta aure shi" *(Jiki Magayi*, sh.10).

Wannan xarsau ne na ban takaici da aka xarsa shi ga mai karatu, saboda mai karatu ya ga irin halin dattaku na Malam Audu mahaifin Zainabu, da kuma yadda yake fargabar za a xauke shi mai magana biyu. Haqiqa hakan a nan gaba zai sa ba wani wanda zai yi masa kallon arziqi a matsayin dattijon qwarai, abin da ya haifar da wannan xarsau shi ne yadda Malam Shaihu a kan neman biyan buqatarsa yake neman sanya Malam Audu cikin wani hali, domin dukkan dattijo na qwarai ba ya son al’umma su yi masa kallon rashin kyautawa musamman zargi a kan kwaxayin dukiya. Haka zalika wannan xarsau ne mai bayyana zahirin rayuwa da kuma abubuwan da suke faruwa a sakamakon dukiya da kuma yadda ake samun dattijai na qwarai masu magana xaya. Mai karatu zai ji takaici ne ba don komai ba, sai don ganin irin halin da Abubakar ya sami kansa a ciki, wanda hakan ya

biyo bayan rashin karva shawara ne daga wajen mahafiyarsa, marubucin littafin ya ci gaba da cewa:

> Da dai suka ga ya sari tafiya sai xaya ya ce, “Tsaya nan”! Abubakar ya tsaya cif, ko xaga qafa bai yi ba, jiki duk na rawa. Da zuwan xam fashin sai ya kafe shi da mari ya kife, ya zare wuqa ya xebe masa rabin kunne, ya bar shi nan (*Jiki Magayi,* sh. 20).

Wannan xarsau ne na ban takaici, domin mai karatu ya ga irin wahalar da Abubakar ya fara fuskanta a kan hanyarsa ta zuwa Sanga. Babu shakka wannan zai xarsa takaici a zuciyar mai karatu musamman idan ya tuna yadda mahaifiyar Abubakar ta ba shi shawara da ma baban Tausayinka-da sauqi a kan ya haqura ya bar wa Allah. Sa’annan kuma ya qi amincewa da haka, wanda hakan ya jawo masa matsala. A nan wajen marubucin ya xarsa wa mai karatu wannan ban takaici ne ta hanyar bayyana masa wahalar da Abubakar ya fara fuskanta wadda shi ya saye ta da kuxinsa. Wannan xarsau ne mai bayyana irin nadamar da dukkan wanda bai yi haquri da rayuwa ba zai iya samun kansa a cikin matsaloli da kuma wahalhalun rayuwa.Marubucin wannan littafi ya yi qoqarin xarsa ban takaici a zuciyar mai karatu ne ta hanyar kawo masa halayyar sata da Idon Matambayi ya sa kansa a ciki kamar yadda ya ce:

> Da idon Matambayi ya gaji da gudu ya zauna ya huta. Bayan ya huta sai ya manta duk wahalar da ya sha a Kafi, wataqila Allah ya ba shi wani xan abu. Sai ya komo chikin Kafi. Da isarsa sai ya buxe qyauren wani qofar gida ya shiga, ya tafi wani xaki a chikin gidan ya iske shi ba qyaure sai tufaniya (*Idon Matambayi*, sh. 32).

Wannan xarsau ne na ban takaici, domin kuwa marubucin wannan littafi ya yi qoqarin jawo hankalin mai karatu ta hanyar xarsa masa ban takaici. Saboda duk wahalar da mai karatu ya karanta a baya cewa Idon Matambayi ya sha a garin Kafi, kuma ya samu ya tsira amma bai haqura ba. Domin kuwa an nuna cewa sai da ya sake komawa cikin wannan gari, ba don komai ba sai don ya fita kunyar 'yan uwansa, yadda suka yi sata suka dawo lafiya shi ma ya yi ya koma musu lafiya. A nan an xarsa wa mai karatu takaici na mummunan halin varawo da bushewar zuciya a kan abin da ba nasa ba. Haka kuma dai, marubucin ya ci gaba da bayyana wa mai karatu irin munanan halayen Idon Matambayi na son sata, wanda hakan zai sanya mai karatu cikin takaici sosai na ganin yadda Idon Matambayi ke gudanar da rayuwarsa, inda ya ci gaba da cewa:

> Da fitar Idon Matambayi gidan Boka ya tafi tiran - tiran bai dire ba sai kasuwa, har inda

> aka zuba kuxin chinikin haja a kan tabarma, ya lababo kamar wanda zai sayi wani turimin sanda. Wuf! Ya duntse tsabar kuxi sulesule ya sheqa a guje ana binsa ana ku tare ku tare. Shi kuma yana kutsawa chikin mutane yana chewa ku tare ku tare, don kada a kama shi (*Idon Matambayi,* sh. 2).

Wannan xarsau ne na ban takaici da marubucin littafin ya yi amfani da shi, domin kuwa a ce yaro kamar Idon Matambayi kamata ya yi a ce yana makaranta yana karatu da aikin taimaka wa iyayensa.Sai ga shi ya qi bin hanya mai kyau ya sanya kansa xaukar abin da ba nasa ba, a nan wajen abin da ya kawo wa mai karatu xarsau na ban takaici shi ne satar da Idon Matambayi ya je ya yi a kasuwa har ta jawo ake binsa da gudu za a kama shi. A nan marubucin ya yi amfani ne da wannan dabara don ya sanya wa mai karatu takaici a zuciyarsa na yadda Idon Matambayi yake neman wargaza rayuwarsa. Ba shakka xarsau ne mai nuna halayya maras kyau don ta zama izina da darasi ga mai karatu a kan ya guji irin wannan xabi'a. A wannan gava kuwa, an sanya wa mai karatu takaici ne don ganin yadda varayi suke fatan samun kayan sata, har ma suke yin addu'a a kan haka, kamar yadda marubucin ya bayyana da cewa:

> Suka che, "Mun gode! Mun gode! Allah kuwa ya xora mu bisa kan masu abu, mu tsiyata mai dukiya; mu sabarta mahukunchi, mu talauta talaka (*Idon Matambayi,* sh. 5).

Wannan batu dai xarsau ne na ban takaici da mawallafin wannan littafi ya xarsa shi ga mai karatu. Domin kuwa haqiqa akwai ban takaici ga mutumin da ba shi da takamammiyar sana'a sai sata. Haka zalika har ma addu'a yake a kan samun nasara, haqiqa furucin da varayin suka yi na roqon Allah a kan ya kawo musu wanda za su tsiyata, wannan shi ne abin da zai xarsa wa mai karatu takaici a zuciyarsa a kan furucin waxannan varayi. Wannan shi ma xarsau ne mai yin hannunka mai sanda da koyar da hali mai kyau da kuma gujewa mummunan hali.Haka dai a wannan gava ita ma, marubucin ya bayyana wa mai karatu wasu abubuwa da suka sanya mai karatu cikin takaicin irin rayuwar da varayi suke gudanarwa, inda ya ci gaba da cewa:

> Da gari ya waye Idon Matambayi ya ga gidan nan da kyar ake ganin rana. Suka tashi suka wanwanke fuskokinsu, suka koma suka zauna. Da hantsi ya soma zafi Xauke ya kawo musu yarwaina haxe da nakiya suka chi. Wajen kusan azahar Qwache ya che, " Ina dabarar abin da za mu yi yau? Mu tafi ne gaba xaya mu uku wurin da mutane suke

> yawan wuchewa, mu lave har Allah ya jefo mana da rabommu?" (*Idon Matambayi,* sh. 6).

Wannan xarsau ne na ban takaici shi ma, marubucin littafin ya nuna yadda varayi suke zama su yi shawara, kuma wai a nasu tunanin abin da suke yi mai kyau ne, tun da dai har suna zaton kayan satar da suke samu rabonsu ne daga Allah. Don haka jin yadda su Idon Matambayi suka haxa shawara a junansu zai sa wa mai karatu takaici a zuciyarsa. Marubucin wannan littafi a qoqarinsa na jawo hankalin mai karatu da xarsa masa takaici a kan yadda varayi suke haxa kansu ba don komai ba sai don su aikata varna su cuci jama'a. Babu shakka mai karatu zai sami kansa cikin takaicin yadda aka nuna rashin imanin da xaya daga cikin varayin nan ya nuna, da kuma dabarar da ta sanya shi aikata haka, inda aka ci gaba da bayyana wa mai karatu yadda ta kasance kamar haka:

> Da ya ga dai ba yadda zai shiga xakin sai wata shawara ta zo masa ta kunna wa xakin wuta. Ya ga idan xakin ya kama wuta ya sami damar yin sata a wani xaki. Daga nan sai ya xauki ashana ya qyatta ya jefa a kan xakin. Shi kuwa ya koma bayan wani xaki ya lave. Kafin a jima kaxan wuta ta kama, mai xaki ya yiwo waje da sauri, yana ihu,

"Wuta! Wuta! Ihu! Ihu!" (*Idon Matambayi,*
sh. 27).

Wannan xarsau ne na ban takaici matuqa, domin kuwa bai ajiye ba bai bayar ajiya ba. Amma ga shi ya zo ya sanya wa xaki wuta don dai ya yi sata. Lallai wannan xarsau ne na ban takaici da aka yi amfani da shi don jawo hankalin mai karatu. Sa'an nan xarsau ne mai daxa fayyace halayyar varawo ta rashin tausayi a kan abin da yake son aikatawa.Waxannan misalai da suka gabata su ne suke qara haska yadda wannan marubuci ya yi amfani da dabarun xarsau don jawo hankalin mai karatu. Haka kuma wannan littafi a mafi yawancin dabarar xarsau da aka fi yawaita amfani da ita za a ga cewa dabarar xarsau ce ta ban takaici da za a iya cewa ita ce mafi dacewa da tsarin wannan littafi. Mai karatu zai fahimci xarsau ne cikin sauqi, ta hanyar karanta misalai da kuma sharhin da aka yi bayan an tsakuro labari daga cikin littafin. Wanda hakan ne yake nuna jumlolin da aka yi amfani da su, har aka samar da xarsau.

#### 4.4.4 Xarsau na ban Mamaki

Marubucin ya jawo hankalin mai karatu ne ta hanyar xarsa masa xarsau na ban mamaki, dangane da bayyana wa mai karatu wani abu da zai sanya shi mamaki kamar haka :

> Ana nan wata rana ya yi mafarki, ya ga wata goxiya a gidan Malam Audu an kai ta kasuwa. Wani mutum kuwa yana sonta qwarai da gaske har ya yi ciniki. Sai shi kuma da ya gan ta ya so ta qwarai kamar me, ya qara kuxi aka sallama masa, ya biya, aka kawo masa gida ya xaure. Wancan kuwa ya haqura tilas. Goxiya tana gidansa har ta haifa masa xan duqushi kyakkyawa wanda kowa ya gani yana sha'awarsa. Da ya yi girma ya isa hawa, ran nan sai ya ce a yi masa sirdi. Aka yi, ya hau ya tafi kilisa. Daga can doki ya abauce ya ka da shi ya tsere, ya bar shi cikin ciwo qwarai (*Jiki Magayi,* sh. 2).

Wannan xarsau ne na ban mamaki, wanda kusan dukkan abin da zai faru a cikin wannan littafi sai da Malam Shaihu aka nuna masa shi a bisa wata siga ta mamaki.Sa'annan kuma bayan da ya farka ya nemi sanin fassarar mafarkin, aka bayyana masa maganar aure har da haihuwa, da ma wahalhalun da ke tattare da auren. Wannan xarsau ne na ban mamaki ga mai karatu, musamman idan ya fara nisa a cikin karanta labarin, zai dinga tuno da mafarkin da Malam Shaihu ya yi. Wannan marubuci ya yi qoqarin jawo hankalin mai karatu da kuma sanya masa xarsau daban-daban, domin a baya kaxan an xarsa wa mai karatu xarsau ne na ban tausayi, sai ga shi ba tare da daxewa ba marubucin ya sake sauya tunanin mai karatu zuwa xarsau na ban mamaki, wannan duk ana yi ne don jawo hankalin mai karatu.

Marubucin littafin Idon Matambayi a qoqarinsa na jawo hankalin mai karatu, ya kawo xarsau na ban mamaki ga mai karatu, a inda ya nuna yadda wani abin mamaki ya faru a cikin labarin kamar haka:

> Idon Matambayi ya zauna, boka ya fita ya bar shi yana jiransa.Bai daxe da fita ba sai Idon Matambayi ya ga xaki ya yi duhu sai ka che da dare. Aka jima chan sai ya ji wani abu ya faso daga bisan xaki sakakaka, bai dai kula ba balle ya ji tsoro. Daga nan sai ya ji dif a kusa da shi a gabansa, kamar wani katon dutse aka sako ya fado. Shiru, shiru shiru, shiru, ba motsi. Daga nan fa jikin Idon Matambayi ya dau rawa farfar, tsoro ya kama shi. Yana chikin wannan hali sai ya ga wayau, dakin duk ya haska da haske, ya chika da kanshin turare. Idon Matambayi ya duba nan ya duba chan, ya ga abin da ya fado kamar dutse na dazu bai gani ba. Yana chikin haka sai ga Boka, ya che, "To, na dawo" (*Idon Matambayi,* sh. 2).

Mai karatu a wannan labari da aka xarsa masa zai cika da mamakin yadda waxannan abubuwa suka kasance. Na farko dai shigowar wani abu cikin wajen da Idon Matambayi ke zaune, wanda mai karatu zai iya hasashen cewa aljannu ne Boka ya turo su. Haka kuma akwai mamaki ga mai karatu a yadda ya ga dauriyar Idon Matambayi da juriyarsa a kan abin tsoron da ya gani, wannan xarsau ne na mamaki, kuma da shi ne mawallafin ya buxe wannan labari a qoqarinsa na jawo

hankalin mai karatu da kuma riqe tunaninsa. Marubucin wannan littafi ya bayyana wa mai karatu irin xauki ba daxin da ake yi da sarkin yaqi Ganxoki tsakaninsa da aljanu da ire-iren abubuwan mamaki da suke faruwa a tsakanin Ganxoki da aljannu. Inda marubucin ya ci gaba da kawo wa mai karatu wannan xarsau na ban mamaki kamar haka:

> Ni kuwa da zuwana sai na faxa fagen fama da dokina ina kirari, ina kabbara da salati. Ga takobi Shafau a cikin hannuna, ga kulkin xan tsofo rataye a kwacciyar sirdina. Da Sarkin nan ya ga haka, sai ya ce wa aljannu su kamo ni. Aljani xari suka taso baki xaya; Nasa Shafau na shafe su, sai kawuna ke faxuwa qum, tim, qum, kamar faxuwar giginya. Sai Sarkinsu ya ce duk su auka, suka yiwo xauki baki xaya (*Ganxoki,* sh. 32).

Wannan xarsau ne na ban mamaki sosai, domin kuwa shi Sarkin yaqi Ganxoki ba aljani ba ne, mutum ne, amma ga shi yana ta yaqi da aljannu yana ta kashe su. Wannan zai xarsa mamaki a zuciyar mai karatu, saboda mai karatu ya san da cewa ba kowane xan adam ba ne zai iya yaqi da aljannu,saboda suna da hanyoyi da dama da za su iya cutar da mutum. Amma ga abin mamaki Sarkin yaqi Ganxoki har su bai bari ba, yana yaqi yana kashe su. Abin da ya haifar da wannan xarsau na ban mamaki shi ne bajintar Ganxoki da kuma yadda yake

yin yaqi har da aljannu.Marubucin wannan littafi ya bayyana wa mai karatu yadda ta kasance tsakanin Sarkin yaqi Ganxoki da Sarkin aljannu, inda yake cewa:

> Da muka farka sai muka ji an dandanne mu, ba mai iya ko numfashi balle magana. Ashe an tashi da mu tsakanin sama da qasa, ba a ajiye mu ba sai a kan tsibirin Sayalana cikin qasar Hindu. Sai ga mu a gaban wani Sarki wanda babu irinsa ga kwarjini da kyaun sarauta. Muka ga jama'a ga su ba fuskar mutane ke gare su ba (*Ganxoki,* sh. 18).

Haqiqa akwai ban mamaki ga abin da ya faru da Sarkin yaqi Ganxoki da xansa Garba Gagare, saboda ga su a qasar Hindu a gaban wasu mutane waxanda fuskarsu ba ta yi kama da ta mutanen da su Ganxoki suka sani ba. Marubucin wannan littafi ya xarsa wa mai karatu xarsau na ban mamaki a kan halin da Ganxoki suka tsinci kansu, haka kuma xarsau ne mai bayyanar da jarumta a kan wani abu da ka iya samun mutum. An xarsa wa mai karatu xarsau na ban mamaki ne ta bayyana yadda wani qaramin tauraro a cikin wannan littafi yake da tsananin qarfi, ta hanyar bayyana wa mai karatu abin da ya aikata da ya sanya xarsau na ban mamaki a zuciyar mai karatu kamar haka:

> Da muka isa garin maza suka shata daga. Da Hambama ya zabura, sai ya figo wani barde daga cikinsu, ya miqa wa 'ya'yansa a hannu ya ce, "Ku yi maza ku babbaka mini shi nan tsakiyar fage in sami abin tavawa". Kafin ya gasu sai ya kama fatar qeya da gurgura, ya fasa qwanya yana sha (*Ganxoki, sh.* 26).

Wannan xarsau ne na ban mamaki, domin yadda kuwa mai karatu da kansa zai sha mamakin yadda Durugu Hambama ke ta yi da arna da yadda suka firgita da al'amarinsa. Wannan xarsau ne na ban mamaki, haka kuma xarsau ne mai nuna yadda marubucin ke son fito wa da mai karatu irin qarfin da Durugu Hambama yake da shi, da kuma tabbatar da nasarar Ganxoki a kan sa. Marubucin wannan littafi ya ci gaba da zaburar da mai karatu ta hanyar sanya masa xarsau na ban mamaki, a inda ya nuna yadda Ganxoki ke yin yaqi da irin bajintar da yake nunawa kamar yadda aka ci gaba da bayyana wa kamar haka:

> Ni kuwa da zuwana sai na faxa fagen fama da dokina ina kirari, ina kabbara da salati. Ga takobi Shafau a cikin hannuna, ga kulkin xan tsofo rataye a kwacciyar sirdina. Da Sarkin nan ya ga haka, sai ya ce wa aljannu su kamo ni. Aljani xari suka taso baki xaya; Nasa Shafau na shafe su, sai kawuna ke faxuwa qum, tim, qum, kamar faxuwar giginya. Sai Sarkinsu ya ce duk su auka, suka yiwo xauki baki xaya (*Ganxoki,* sh. 32).

Wannan xarsau ne na ban mamaki sosai, domin kuwa shi Sarkin yaqi Ganxoki ba aljani ba ne, mutum ne, amma ga shi yana ta yaqi da aljannu yana ta kashesu. Wannan zai xarsa mamaki a zuciyar mai karatu, saboda mai karatu ya san da cewa ba kowane xan Adam ba ne zai iya yaqi da aljannu, saboda suna da hanyoyi da dama da za su iya cutar da mutum. Amma ga abin mamaki Sarkin yaqi Ganxoki har su bai bari ba, yana yaqi yana kashesu. Abin da ya haifar da wannan xarsau na ban mamaki shi ne bajintar Ganxoki da kuma yadda yake yin yaqi har da aljannu, kuma hakan zai sa mai karatu jin matuqar qaunar babban tauraro a zuciyarsa, musamman yadda marubucin littafin ya ba shi qarfi da nasara a kan duk wani yaqi da ya tunkara, don haka mai karatu ba shi da wata qiyayya da zai ji yana yi wa babban tauraro a sakamakon halayensa na birgewa da taimako. Haka kuma mai karatu zai ji takaicin yadda Sarkin Aljanu ya sa a yi xauki gaba xaya wajen halaka Ganxoki.

### 4.4.5 Xarsau na ban Tsoro

Marubucin wannan littafi ya xarsa wa mai karatu xarsau na ban tsoron abin da zai faru a kan Idon Matambayi, domin duk da irin halayyarsa ta kasancewa varawo, hakan bai hana mai karatu jin tsoron abin da zai same shi ba. An ci gaba da kawo wannan labari kamar haka:

> Ya hangi wata itachiya mai inuwa liflif, ya tafi gindinta ya zauna. Ashe bai sani ba chewa hanyan nan ta 'yamfashi che, tun ba lokachin da rana ta take a tsaka ba. Yana nan zaune sai ya ga kibiya ta dira a gabansa dik. Ya duba gabas, ya duba arewa, ya duba kudu, ya duba yamma, bai ga kowa ba. Ya xaga kansa dai bisa, sai ya ga mutane guda biyu a kan wani reshe mai 'yar dufuwa, kowane da kwari a rataye, da baka da kibiya a xane (*Idon Matambayi,* sh. 3).

Wannan xarsau ne na ban tsoro da aka yi amfani da shi a wannan littafi, don jawo hankalin mai karatu dangane da karanta littafin. Haqiqa mai karatu zai ji an xarsa masa tsoron bai san waxanda suka harbo wa Idon Matambayi kibiya abin da suke nufi ga Idon Matambayi ba. Sa'annan kuma an fayyace wa mai karatu cewa a inda Idon Matambayi ya zauna hanya ce ta ' yanfashi, don haka mai karatu zai ji an xarsa masa tsoro a kan abin da ya faru tsakanin Idon Matambayi da mutanen nan da suka harbo masa kibiya. Marubucin wannan littafi shi ma ya yi qoqari wajen sauya tunanin mai karatu lokaci zuwa lokaci ta hanyar sanya masa xarsau daban-daban don riqe tunaninsa.

Mai karatu zai sami kansa cikin tsoron abubuwan da za su biyo baya a sakamakon abin da Ganxoki ya aikata kamar yadda aka bayyana a nan:

> Ana nan cikin zaman lumana, sai wani Bature ya shiga Gidan Sarki, ba tare da izninsa ba. Sai Sarki ya sa ni na tsunke masa kai da takobi. Wannan abu fa ya sake ta da zaune tsaye. Na ce, " Kai oho, ina rowan Ganxoki!" Da Sarki ya ga abin da ya sa aka yi ba daidai ba ne, ya zama kamar warwarewar amana ce, sai ya fita ya nufi Lafayi daga nan, har Kafi. Ya dai rasa inda zai sa kansa, domin kowa ka gani cikinsa ya xuri ruwa saboda tsoro a wannan zamani (*Ganxoki,* sh. 5).

Wannan xarsau ne na ban tsoro, domin dai marubucin ya yi qoqarin jawo hankalin mai karatu ta hanyar xarsa masa tsoron abin da zai iya zuwa ya je ya zo, tun da dai Ganxoki ya tsinke kan Bature lokaci guda bisa umarnin Sarki. Lallai wannan abu zai xarsa tsoro a zuciyar mai karatu dangane da abin da zai iya samun Sarki da ya sa aka aikata wannan ta'asa ko kuma shi Ganxokin da ya aikata. Saboda hukuncin da aka xauka ya yi zafi da yawa kuma yana da ban tsoro.Wannan xarsau ne da marubucin littafin ya yi amfani da shi wanda ko a gaba idan mai karatu ya ci karo da wani abu da aka ce Ganxoki ya yi ba zai samu shakku a zuciyarsa ba, domin ya san halin Ganxoki.

#### 4.4.6 Xarsau na Farin Ciki

An sami xarsau na farin ciki a wannan gava ne, a sakamakon yadda mai karatu ya daxe yana karanta yadda taurarin cikin littafin suke aikata sata da kuma jin takaicin haka. Babu shakka wannan ya jawo hankalin mai karatu ta hanyar xarsa masa farin cikin yadda a qarshe rayuwar su Idon Matambayi ta koma kamar yadda ya ci gaba da cewa:

> Idon Matambayi ya koma gidansu ya yi ta jin dadi.Bai yi wata guda da zuwa ba sai gobara ta tashi a kusa da gidansu da rana kata, ta kone gidan makwabtan da na su Idan Matambayi, kayansa suka kone, kudinsa suka lalache, ya koma ba wuri ba wurin zama" (*Idon Matambayi,* sh. 48).

Mai karatu ya karanta a baya, ya san irin abubuwa mara sa kyau da Idon Matambayi ya aikata a rayuwarsa, wanda hakan ne ya janyo ba shi da farin jini a wajen mai karatu saboda munanan xabi'unsa. Don haka wannan abu da ya sami Idon Matambayi lallai abin farin ciki ne ga mai karatu, domin marubuci na sane da irin cutar da al'umma da suka yi. Wannan xarsau ne da marubucin littafin ya kammala labarinsa da shi, kuma ba shi ba ne xarsau xin da aka fara littafin da shi ba, kuma ba shi ne wanda ya fi mamaye littafin ba. Mai karatu a wannan gava an xarsa masa farin ciki ne ta hanyar bayyana masa

yadda wata tauraruwar littafin ta kuvuta ta hanyar Ganxoki, inda ya ci gaba da cewa:

> Ya tashi ya durqusa ya ce, "Na rantse da Allah da addinin da ka sani, ban santa ba, ba kuwa wanda ya san ta tsakanin mutum ko aljan. Yarinya ta tashi ta yi gaisuwa da kanta guna. Na ce mata, "Bari kuka, kya koma gida, in Allah ya so. Ni ma ina da nufin komawa Sakkwato, daga can har Kwantagora". Da ta ji haka sai ta ce, "Ai kuwa su ma 'yanuwammu ne bisa ga abin da na ke ji, duka asalimmu xaya da su". Na ce, "I, hakanan ne" (*Ganxoki,* sh. 22).

Wannan xarsau ne na farin ciki da marubucin littafin ya yi qoqarin jawo hankalin mai karatu, ta hanyar nuna masa yadda Sarkin yaqi Ganxoki ya yi alqawarin mayar da yarinyar nan gida wajen iyayenta. Haka kuma ba a daxe ba aka ga ya mayar da ita gida. Wannan ne yake nuna mana cewa xarsau ne na farin ciki, domin kuwa mai karatu ya ga an kuvutar da wannan yarinya, wanda hakan zai qara sa wa mai karatu wani farin ciki a zuciyarsa bisa halin nagartar babban tauraro bisa ga yadda yake qin zalunci.

Haqiqa marubutan waxannan littattafai sun yi amfani da dabarun xarsau masu yawa kuma mabambanta don jawo hankalin mai karatu bisa fahimtar saqonnin manufofin littattafansu.

### 4.4.7 Xarsau ‘yan Tagwai

Xarsau ‘yan tagwai dai qoqari ne na wannan bincike, domin na lura da cewa marubuta waxannan littattafai sun qulla dabarar xarsau guda biyu a lokaci guda. Daga jin wannan kalma ta ‘yan tagwai za a fahimci Xanjuma ne da Xanjummai. A wannan bincike an lura da yadda marubuta waxannan littattafai suke haxa xarsau guda biyu. Sai dai a mafi yawanci akan jinginar da xarsau guda xaya ne ga babban tauraro, daga nan kuma sai a jinginar da xayan tauraron ga qaramin tauraro ko kuma qananun taurari. Marubuta littafin *Jiki Magayi* sun yi amfani da irin wannan xarsau a wasu wurare na cikin littafinsu kamar haka:

> Da gari ya waye Kyauta ya tashi. Bayan ya wanke ido ya yi salla ya shiga ya gaida ubansa da uwa tasa, ta ba shi karin kumallo, ya ce za shi makaranta. Ya fita sai xakin ubansa,ya iske kuxi a zube a buzu, uban kuwa ya fita qofar gida. Sai ya sa hannu ya xebi sule biyu ya fita abinsa. Maimakon ya tafi makaranta sai ya guje wa abokan zuwansa ya shiga gari, ya kashe kuxinsa (*Jiki Magayi,* sh. 30)

A wannan gava, mai karatu zai tsincin kan sa ne a cikin takaicin yadda Abubakar ya yi asiri na lalata Kyauta xan Malam Shaihu. Haka kuma zai ji tausayin yadda rayuwar Kyauta za ta kasance.Wannan xarsau ne ‘yan tagwai, dalilin kasantuwarsu tagwaye shi ne yadda a lokaci guda aka gwama tunanin mai karatu ta hanyar xarsa masa xarsau mabambanta a lokaci guda. Wannan dabara ce mai koyar da darasin rayuwa mai yawa, domin kuwa za a ga cewa a baya Kyauta yaro ne mai xabi’u masu kyau, sai kuma ga shi qaddarar rayuwa tana neman jefa shi a cikin halaye waxanda ba a san shi tun asali da su ba.Marubucin wannan littafi, ya yi qoqarin xarsa wa mai karatu xarsau na ban takaici ne ta hanyar kawo masa irin yadda Abubakar ya qeqasa qasa a kan qin bin shawarar mahaifiyarsa da kuma qudurinsa na barin mahaifiyarsa da ‘yan ‘uwansa a kan neman fansa. Haka dai marubucin ya ci gaba da cewa kamar haka :

> Ya ce mata, " Haba, iya idan ni xam mutum biyu ne, sai na rama. Zan shiga duniya, da ko wane hali na sani Allah zai taimake ni. Amma kada ki damu. Ga Audu nan da qanwata da kakarmu, sun ishe ki zaman duniya, ni kuwa idan da rai wata rana za ki ga na komo *(Jiki Magayi,* sh.9).

Wannan xarsau ne na ban takaici da marubucin wannan littafi ya xarsa shi ga mai karatu. Don kuwa mai karatu ya ga dai abin da ya faru ga Abubakar, kuma mahaifiyarsa ta yi masa nasiha, ta ce ya sami wata daidai da shi. Sai dai sam, Abubakar bai yi na'am da abin da mahaifiyarsa ta gaya masa ba. Mai karatu zai ji an xarsa masa takaicin alwashin da Abubakar ya xauka har kuma da niyyar ya bar gida. Shi bai damu ba zai dawo ya tarar da mahaifiyarsa da rai ko kuma ba zai dawo ya tarar da ita ba. Haka nan marubucin littafin ya yi amfani da wannan dama ya xarsa wa mai karatu xarsau na ban tausayin mahaifiyar Abubakar domin ga xan da ta haifa yana gaya mata cewa zai bar ta ya shiga duniya ga qannensa nan sun isheta rayuwa.Wannan dabara ta gwama xarsau guda biyu ba ta tsaya a nan ba, domin kuwa an same ta a cikin littafin *Idon Matambayi* kamar haka:

A nan, marubucin littafin ya fara kawo wa mai karatu xarsau na ban tausayi ne a kan yadda su Idon Matambayi suke nuna rashin kyautawa ga matafiya da tare hanya da aikata qwacen dukiyar da ba su san yadda aka same ta ba. Marubucin littafin ya ci gaba da kawo labari mai xauke da xarsau na ban tausayi haxe da takaicin halayen waxannan varayi kamar haka:

> Mutane duk suka yi shiru, kowa jikinsa yana rawa, sai wani matsorachi a chikinsu ya che," Mun ji. To, nawa za mu ba ka?" Yayin da duk ake wannan abu Qwache yana lave yana jin abin da suke yi. Su kuwa ba su san yana nan ba. Idon Matambayi ya che, "Duk kayan jakunanku za ku sauke ku tafi". Suka che "To". Suka yi ta sauke kaya, kowa yana kora jakinsa yana tafiyarsa (*Idon Matambayi,* sh. 8).

Wannan xarsau ne na ban tausayi, domin su dai varayin nan ba su san ta yadda waxannan mutane suka tara dukiyarsu ba. Ga shi sun yi wo tafiya ba su san takamaimai ma daga ina suke ba, amma ga su Idon Matambayi sun dage a kan sai sun ajiye dukkan kayansu sun tafi. Abin da ya haifar da wannan xarsau na ban tausayi ga mai karatu shi ne, yadda marubucin littafin ya nuna rashin imanin varayin nan da suka tare waxannan matafiya. Hasali ma mai karatu baya ga jin tausayi na waxannan mutane zai sake jin xarsau na ban takaici a kan halayyar da varayin nan suka nuna ga waxannan matafiya. Don haka akwai tausayi na matafiya da jin takaicin mummunar halayyar varayi duk a lokaci xaya, wannan dabara ce da marubucin ya yi amfani da ita don ya jawo hankalin mai karatu ya ci gaba da karanta wannan littafi. Domin kuwa abu ne mai yiwuwa da mai karatu zai sanya a ransa cewa duk waxannan munanan ayyuka da su Idon Matambayi suke aikatawa

a gaba za su girbi abin da suka shuka. Haqiqa mai karatu zai sami xarsau na ban dariya a kan ganin yadda varayin nan suka gamu da gamonsu domin sun taro wanda ya fi su. Marubucin littafin ya yi qoqarin xarsa wa mai karatu xarsau na ban dariya da kuma mamakin xaya daga qananan taurari ta yadda ya fi qarfin sharrin varayi kamar haka:

> Da jin haka sai Qwache ya zaro wuqa zai dava wa mutumin sai hannunsa ya sage. Xauke kuma ya rugo da gudu ya kama shi da kokuwa, sai jikin mutumin ya riqa bin Xauke kamar wanda yake jan alewa. Idon Matambayi ya kai masa irin qullin nan nasa a chiki, sai hannunsa ya dafe. A'a Mutumin nan dai yana kallon qoqarin kowa a banza. Ya tambaye su ya che, " In che ko yanzu kun san ku ba kowan kowa ba ne?" "I, mun sani, kowa da wanda ya fi shi" (*Idon Matambayi,* sh. 20).

Wannan xarsau ne na ban dariya, domin marubucin wannan littafi ya yi qoqarin jawo hankalin mai karatu ta hanyar xarsa masa xarsau na ban dariya a wannan shafi. Domin kuwa an nuna yadda su Idon Matambayi suke yunqurin dukan mutumin da suka haxu da shi, amma da kansu suka haqura suka tabbatar da cewa duk abinka akwai wanda ya fi ka. A xaya vangaren kuma, xarsau ne na mamaki sosai, domin mai karatu da farko yana zaton varayin nan za su iya yin nasara a kan

wannan mutumi, sai ga shi kallo ya koma sama a inda mai karatu ya ga yadda ta kasance shi ne zai sanya shi cikin mamaki.

Haka kuma marubucin littafin *Ganxoki* ya yi amfani da irin wannan dabara a inda ya ce:

> Da gari ya waye mazaje suka yi karo, sai ka ce yankin dutse ke gamuwa, suka ja da baya suka gwabza, mutanen Inkwai suka yi xai xai, rabinsu duk sun kai takarda. Waxanda suka koma suka ba Sarkinsu labari. Ya ce "Mutuwa kuka gudo wa, ita kuka tarar." Ya sa duk aka kashe su. Ya ce, "Gobe wani kuma ya gudu ya ce zai kai labari!" (*Ganxoki,* sh. 27).

Wannnan xarsau ne na ban tausayi, domin kuwa sun gudu don ceton rai, sa'annan sun zo inda suke ganin za su tsira, amma an kashe su. Wannan dabara ce da marubucin wannan littafi ya yi amfani da ita don jawo hankalin mai karatu da xarsa masa tausayi a cikin ransa. Haka kuma abin da ya xarsa wannan tausayi a zuciyar mai karatu shi ne kisan nan da aka yi wa waxannan mayaqa da suka ga za a kashe su, suka dawo aka kuma kashe su a inda suke tsammanin samun tsira da mafaka. A xaya vangaren kuwa duk dai a lokaci xaya, xarsau ne na ban takaicin halayyar wannan Sarki ta zalunci ga wanda ya yi qoqarin tseratar da kan sa amma sai ga shi ya halaka su.

### 4.4.8 Xarsau na Gangan/Zulaqe

Xarsau na gangan shi ma wannan bincike ne ya lura da cewa akan iya samun nau'insa a cikin waxannan littattafai da aka gudanar da bincike. Marubucin littafin *Ganxoki* ya yi amfani da irin wannan xarsau wanda da zarar mai karatu ya ci karo da shi ya san da wahala abin ya iya faruwa a rayuwa ta zahiri.Don haka ne ya zama xarsau na zulaqe. Misalin wannan xarsau a littafin *Ganxoki* shi ne inda aka ce:

> Da muka isa garin maza suka shata daga. Da Hambama ya zabura, sai ya figo wani barde daga cikinsu, ya miqa wa 'ya'yansa a hannu ya ce, "Ku yi maza ku babbaka mini shi nan tsakiyar fage in sami abin tavawa". Kafin ya gasu sai ya kama fatar qeya da gurgura, ya fasa qwanya yana sha (*Ganxoki,sh.*26).

Wannan xarsau ne na ban mamaki, domin yadda kuwa mai karatu da kansa zai sha mamakin yadda Durugu Hambama ke ta yi da arna da yadda suka firgita da al'amarinsa. Haka kuma xarsau ne mai nuna yadda marubucin ke son fito wa da mai karatu irin qarfin da Durugu Hambama yake da shi, da kuma tabbatar da nasarar Ganxoki a kan sa. A nan shi kan sa mai karatu ya san an yi amfani da xarsau na zulaqe, domin kuwa dai a ce mutum yana fasa kwanya yana sha, kuma ta baraden da ake ganin sun kai sadaukai a fagen yaqi.

Marubucin wannan littafi ya ci gaba da zaburar da mai karatu ta hanyar xarsa masa xarsau na zulaqe mai ban mamaki, a inda ya nuna yadda Ganxoki ke yin yaqi da irin bajintar da yake nunawa kamar yadda aka ci gaba da bayyana wa kamar haka:

> Ni kuwa da zuwana sai na faxa fagen fama da dokina ina kirari, ina kabbara da salati. Ga takobi Shafau a cikin hannuna, ga kulkin xan tsofo rataye a kwacciyar sirdina. Da Sarkin nan ya ga haka, sai ya ce wa aljannu su kamo ni. Aljani xari suka taso baki xaya; Nasa Shafau na shafe su, sai kawuna ke faxuwa qum, tim, qum, kamar faxuwar giginya. Sai Sarkinsu ya ce duk su auka, suka yiwo xauki baki xaya (*Ganxoki,* sh. 32).

Wannan xarsau ne na ban mamaki sosai, domin kuwa shi Sarkin yaqi Ganxoki ba aljani ba ne, mutum ne, amma ga shi yana ta yaqi da aljannu yana ta kashesu. Wannan zai xarsa mamaki a zuciyar mai karatu, saboda mai karatu ya san da cewa ba kowane xan Adam ba ne zai iya yaqi da aljannu, saboda suna da hanyoyi da dama da za su iya cutar da mutum. Amma ga abin mamaki Sarkin yaqi Ganxoki har su bai bari ba, yana yaqi yana kashesu. Abin da ya haifar da wannan xarsau na ban mamaki shi ne bajintar Ganxoki da kuma yadda yake yin yaqi har da aljannu. Haka kuma a xaya vangaren mai karatu zai ji

an yi amfani da zulaqe ne don nuna masa irin girman da Ganxoki yake da shi da kuma kambama shi da marubuci yake yi a cikin littafinsa. Don haka za a iya cewa ya zama xarsau ne na kambame wanda a rayuwa ta zahiri ba lallai ne a ce mutum ya sami nasara mai yawan haka a kan aljannu ba. Wannan ne zai sanya zuciyar mai karatu faxawa cikin shakkun yadda hakan za ta kasance, duk kuwa da cewa an xarsa masa mamaki, amma ya san ba lallai ya kasance hakan mai iya faruwa ba ne a rayuwa ta zahiri.

### 4.4.9 Xarsau Jirwaye da Ba-xoki

Xarsau jirwaye da ba-xoki nau'i ne daga cikin nau'ikan dabarun jawo hankali, da marubuta suke yin amfani da su don cim ma burinsu a kan masu karanta littattafansu.Wannan bincike ya lura da cewa akan sami wannan nau'i na gwama ba-xoki da xarsau jefi-jefi a cikin waxannan littattafai,da aka gudanar da nazari a cikinsu. Daga cikin wuraren da aka yi amfani da wannan nau'i na jirwayen ba-xoki da xarsau akwai waxannan:

Sai ya sa hannu cikin ratayensa, ya ce:
Ga wannan ka kai masa, da ganinta ya sani.

> In ka tafi ka gaya dukan labarina ka ce ina gaishe shi ina kuwa da rai. Ina kuwa so ya

> yafe mini dukan irin dangin abin da na yi masa *(Jiki Magayi, sh.14)*.

Wannan xarsau ne gwauraye da ba-xoki, domin kuwa marubucin bayan ya jefa zaquwar ba-xokin tafiyar Abubakar zuwa wajen mahaifin Tausayinka-da sauqi, sai ya zama cewa akwai vurvushin tausayin nadamar da Tausayinka-da sauqi ya yi, dangane da neman gafarar mahaifinsa. Wannan nau'I ne na xarsau mai jirwaye da ba-xoki, haka kuma yana koyar da mai karatu muhimmancin iyaye da neman yafiyarsu a kan wani laifi da aka yi musu.

A nan mai karatu zai ga cewa, an jirwaya dabaru guda biyu a lokaci guda. Wato dabarar xarsau da ta ba-xoki, inda marubucin yake cewa :

> Sai ya yi sallama, ya tashi. Bai xauki kome daga cikin gidan ubansa ba,ko guzuri, ya tafi Kwanci tashi har ya kai Garuje. Ya tafi wurin uwarsa ya gaya mata dukan abin da ya faru Ya ce, "Yanzu ya kamata in koma da ke gida, Ki yi zamanki can cikin danginki" *(Jiki Magayi,* sh. *50)*.

Wannan na nuna yadda marubucin wannan littafi na *Jiki Magayi* ya jirwaya ba-xoki da xarsau a waje xaya. Mai karatu a nan zai ji an xarsa masa tausayin Abubakar dangane da nadamarsa da kuma tausayin ita kan ta mahaifiyar tasa. A xaya vangaren kuma, mai karatu zai so ganin abin da aka

baxokanta masa na komowar mahaifiyar Abubakar gida abu ne mai yiwuwa ko akasin haka. Wannan shi ne yadda marubucin ya garwaya dabaru guda biyu a lokaci guda, da shirya su a zuciyar mai karatu.

Marubucin wannan littafi ya yi amfani da dabaru guda biyu a lokaci guda. Mai karatu zai ji son ganin abin da zai faru idan mutane suka tafi neman varayin nan. Haka kuma zai ji tsoron abin da zai iya faruwa a lokacin d mutanen garin nan suka yi xauki zuwa mavoyar varayi. Ga dai yadda ta kasance kamar haka:

> Manyan gari suka yi shiru. Chan wani ya che, " Ranka ya daxe, yanzu abin da za mu yi sai ka sa a yi shela, dukan wanda ya sani da shi xanfarauta ne ya zo, da kuma tsofon mayaqi. Idan sun zo mu hau dawaki mu bi hanyar Dutsen Sauke- mu- raba, inda Sani ya che wataqila suna nan, tun bai mutu ba *(Idon Matambayi,* sh. 33).

Haqiqa mai karatu zai sami kan sa a cikin jirwayar dabarun guda biyu na ba-xoki da xarsau, domin kuwa baya ga zaquwa da ganin yadda wannan tafiya za ta kasance da aka sanya wa mai karatua zuciyarsa, domin kuwa hakan bai hana a xaya vangaren mai karatu ya ji xarsau na ban tsoron idan ba a sami nasarar kama varayin nan b aba a san abin da zai faru ba. Wannan dabara ce guda biyu a haxe ta ba-xoki da xarsau da take nuna mana zamantakewar

rayuwa ta haxin kai a tsakanin al'umma.Mai karatu zai sami kan sa a cikin jirwayen dabaru guda biyu a lokaci guda kamar haka :

> Kafin mu kai wani aljani kuma ya ba uban labari cewa xansa ya musulunta. Sai ya yi fushi. Da zuwammu ya sa aka xaure xan, ya ce a tafi da ni wani ruwa wanda ya ke horo da shi a jefa. Sanyinsa ya fi qanqara. Sauran kamar sa'a xaya kafin a kai ga ruwan nan sai Allah ya nufi aljanin nan da gajiya, ya sauke ni don ya huta, sai barci ya share shi. Na sance kaina, na nemo babban dutse na kwantara wa aljanin a ka, kai ya ratsatstsake ya mutu (*Ganxoki,* sh. 40)

Wannan xarsau ne gauraye da ba-xoki, domin kuwa mai karatu zai sami kansa cikin son ganin yadda Ganxoki zai kuvuta, musamman ganin cewa waxanda suke tsare da shi aljannu ne. A inda a xaya vangaren kuma,zuciyar mai karatu za ta cika da xarsau na farin cikin kuvutar Ganxoki. Wannan xarsau ne mai koyar da mu rashin yanke qauna daga rahmar Ubangiji, kamar yadda bayan da aka kama Ganxoki Allah ya kuvutar da shi.

A nan an yi amfani da ba-xoki da xarsau a lokaci guda kamar haka :

> Da muka farka sai muka ji an dandanne mu, ba mai iya ko numfashi balle magana. Ashe an tashi da mu tsakanin sama da qasa, ba a ajiye mu ba sai a kan tsibirin Sayalana cikin qasar Hindu. Sai ga mu a gaban wani Sarki

> wanda babu irinsa ga kwarjini da kyaun sarauta. Muka ga jama'a ga su ba fuskar mutane ke gare su ba (*Ganxoki,* sh. 18).

Mai karatu zai ji an xarsa masa ba-xokin ganin yadda za ta kasance a tsakanin Ganxoki da Sarki dangane da kawo kan Durungu Hambama. Haka kuma a xaya vangaren mai karatu zai cika da tausayin makircin da aka qulla masa, haka kuma mai karatu zai ji an xarsa masa tsoron abin da zai iya faruwa ga Ganxoki.

### 4.5 Naxewa

A wannan babi an kawo ba-xoki da xarsau a littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki*. Haka kuma an kawo tarken matanonin waxannan littattafai ta yadda aka gano yadda waxannan marubuta suka sarrafa tunaninsu wajen amfani da dabarun ba-xoki da xarsau a cikin waxannan littattafai.

## BABI NA BIYAR

## KAMMALAWA

### 5.1 Gabatarwa

Wannan babi yana qunshe da bayanan kammalawa na wannan bincike. Wato gudunmawar bincike da aka bayyana yadda binciken ya gano tare da fito da wasu abubuwa da binciken ya gano, a matsayin gudunmawar binciken da kuma iyakancewar bincike da shawarwari.

### 5.2 Gudunmawar Bincike

Wannan bincike ya bayar da gudunmawa sosai, musamman ta fuskar gano tare da fito da abubuwan da wannan bincike ya gano. Wannan bincike ya gano cewar dukkannin qagaggun labaran da aka gudanar da bincike a cikinsu, sun yi amfani da wannan dabara ta ba-xoki don jawo hankalin mai karatu, sai dai kowannensu akwai inda ya fi karkata wajen amfani da ba-xokin, duk da dai cewa binciken ya gano kowannensu akwai hanyoyin da yake bi wajen qulla zaren wannan dabara ta ba-xoki.

Wannan bincike ya bayar da gudunmawa wajen kawo wasu nau'ika na xarsau da ya gano, ya kuma fito da su a cikin qagaggun labaran da aka gudanar da nazari a cikinsu. An bincika daga dukkan waxanda suka yi bincike a kan abin da ya shafi ba-xoki da xarsau, ba a sami cin

karo da wani manazarci da ya fito da kwatankwacin abin da wannan bincike ya sami nasarar fitowa da shi ba, wanda ya shafi xarsau, domin kuwa binciken ya zaqulo wasu nau'ika na xarsau da ba-xoki, waxanda babu wani nazari da aka ci karo da shi, da ya fito da su. Waxannan nau'o'in ba-xoki da xarsau su ne kamar haka :

Ba-xoki jirwaye ko gauraye da xarsau

Xarsau 'yan tagawai

Xarsau na zulage ko na gangan.

Dukkannin waxannan nau'ika an yi qoqarin samo su a cikin waxannan littattafai, wanda hakan ne ya zama gudunmawa ga wannan bincike.

Binciken ya bayar da gudunmawa ta fuskar xorawa daga inda manazrta suka tsaya, ta fuskar bincike a kan abin da ya shafi ba-xoki da xarsau. Sa'annan binciken zai ci gaba da bayar da gudunmawa ga sauran manazarta da 'yan uwana xalibai, domin ta bin sahun wannan bincike za su sami damar ci gaba da bincike daga inda aka tsaya.

A qarshe, binciken ya bayar da gudunmawa wajen sake fito da muhimmancin ba-xoki da xarsau, ta hanyar bayyana yadda suka taka rawa wajen isar da saqonnin waxannan littattafai na *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki.*

### 5.3 Iyakancewar Bincike

Wannan bincike an iyakance shi ne a kan ba-xoki da nau'o'insa, wato ba-xokin gaske na kusa da na nesa da kuma ba-xokin gangan. Sa'annan an duba xarsau da ire-irensa kamar xarsau na ban tsoro da na farin ciki da na takaici da na ban tausayi da ban dariya da kuma xarsau na ban mamaki. Wannan bincike an iyakance shi ne a kan zavavvun qagaggun labarai guda uku, wato littafin *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki*. Nazarin dai bai duba wasu dabaru ba bayan na ba-xoki da xarsau, haka kuma a cikin qagaggun labarai aka tsamo dabarun kaxai, ba tare da tsamo su daga wasan kwaikwayo ko waqa ba.

### 5.4 Shawarwari

Dangane da shawarwari bayan gudanar da wannan bincike da kuma abubuwan da aka fito da su a cikin wannan bincike, hakan ya ba da damar bayar da shawarwari kamar haka:

- Haqiqa yana da kyau manazarta su ci gaba da qoqari wajen zaqulo dabarun da mawallafa qagaggun labarai suke amfani da su don jawo hankalin mai karatu. Domin kuwa ta haka ne za a dinga fahimta da fayyace irin ximbin hikimomin da ke tattare da

labaransu, wanda hakan zai daxa taimakawa wajen bunqasar ayyukan adabin Hausa.

- Akwai buqatar yin zuzzurfan nazari makamancin wannan, ba yawanci a dogara kacokan a fi ba wa wani vangare na adabi, irin su waqa ko was an kwaikwayo qarfi ba. Alal- haqiqa sauran vangarorin suna da ximbin hikimomi da za a iya samu a cikinsu waxanda za a iya fitowa da su don cigaban adabin al'ummar Hausawa.

- Haka kuma yana da kyau faxaxa bincike a kan sauran dabarun jawo hankali kamar su amfani da addini da al'ada, da hoto cikin bayani da dai sauransu.

## 5.5 Kammalawa

Wannan bincike da aka gudanar ya tattaro bayanai ne dangane da yadda marubuta littattafan *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki* suka shirya dabarun jawo hankalin mai karatu. Haka kuma binciken ya kawo bayanai tun a babi na farko da suka haxa da muradai da dalilai da manufa da tambayoyin bincike da farfajiya da ra'in da aka xora bicike, da kuma tarihin marubuta waxannan qagaggun labarai na *Jiki Magayi* da *Idon Matambayi* da *Ganxoki.*

Haka kuma babi na biyu ya qunshi bitar ayyukan da suka gabata ne.Sai kuma babi na uku da ya qunshi hanyoyin gudanar da binciken da kuma babi na huxu wanda aka bayyana yadda aka sami ba-xoki da xarsau a cikin waxannan littattafai ta hanyar gudanar da tarken matanonin littattafan. A qarshe binciken ya bayyana abubuwan da ya gano a matsayin gudunmawar bincike da kuma iyakancewar bincike da shawarwari.

**MANAZARTA**

Aisha, M.M.K. (2018). “Tarken Tsari a Littafin Wasan Kwaikwayo na *Kishi ko vata*. Kundin Digiri na Xaya. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Aliyah, A. (2009). “Rupert Moultrie East: Gudunmawarsa kan adabin Hausa". Kundin Digiri na Uku. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero, Kano.

Asiya, M.N. (2012). *Magana jari ce (1-3):* Nazarin Salo da Sarrafa Harshe. Kundin Digiri na Uku.Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Applebee, N. (1997). *The language of literature*. United State of America: Mc Dougal Littell.

Bello, W.K.A. (1968). *Ganxoki*. Zariya: NNPC.

Binta, A. (2014). “Kwatanta Salon Harshe a Littafin Wani Hanin ga Allah da na Budurwar Zuciya”Kundin Digiri na Biyu. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Blau, S. (1998). *The Writer’s cCaft.* United State of America: Mc Dougal Littell

Booth, A. (2005). *The Norton Introduction to Literature.* New York: W.W. Norton and Company.

Brewer, W.F. (2013). *The Nature of Narrative Suspense and the Problem Rereading*. University of Illinois Urbana-Champaign.

Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya (2006). *Qamusun Hausa na Jami’ar Bayero*. Zaria: ABU Press.

Xangambo, A. (2008). *Rabe-raben Adabin Hausa.* Zaria: Amana Publishers Limited.

Xanja, H.K. (2013). "Nazarin Salon Harshe A Littafin Tsumagiyar Kan Hanya na Musa Muhammad da Zavi Naka na Munir Mamman Katsina" Kundin Digiri na Biyu. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Fatima, I.M. (2012). Nazarin Gina Halaye na Gari a Rubutattun Qagaggun Labarai na Gasar (1933) da ta (1980). Kundin Digiri na Biyu. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. (2009). Muhimman Gasanni Waxanda Suka Daxa Bunqasa Rubutun Zube' Takarda Wadda ya Gabatar. Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zaria.

Gwarzo, M.S. (1968). *Idon Matambayi.* Zaria: NNPC

Habiba, A.U. (2014). "Kwatanta Salo da Sarrafa Harshe a Waqar Mikiyar Zuhudu da Littafin *Mace Mutum*. Kundin digiri na biyu. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Higdon, M. J. (2009). The Use of Fore-shadowing as a Persuassive Device in Judicial Narrative. https://heinonline.org

Qamariyya, A.A. (2018). "Kwatanta Dabarun Jawo Hankali da Salon Sarrafawa a Littafin *Ta cuce ni* da *Saba Xansabi*. Kundin Digiri na Uku. Kano : Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Kirszner, and Mandell, (2007). *Literature. Reading. Reacting. Writing*. United State of America: Thomson Wadsworth.

Kiyawa, H.A (2006). "Kwatanta Salon Littattafan Qagaggun Labarai na Maje El-Hajeej da na Nazir Adam Salih". Kundin Digiri na Biyu. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Muhammad, A.U. (2011). "Nazari A Kan Littafin Duniya Budurwar Wawa na Xanfulani" Kundin Digiri na Xaya.Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Muhammad, S.A. (2007). "Magana Zarar Bunu: Nazarin Salo a Littafin so Aljannar Duniya.Kundin Digiri na Xaya. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Muhammad, S.T. (2014). "Tasirin amfani da kalmomin aro wajen isar da saqo cikin qagaggun labaran Hausa: Tsokaci kan littafin Ganxoki na Bello Kagara da Duniya Budurwar Wawa na

Xanfulani" Kundin Digiri na Xaya. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Mukhtar, I. (2010). *Jagoran nazarin qagaggun labarai* (Tsari na uku). Kano: Iya Ruwa Publishers.

Mukhtar, I. (2012).Wasu dabarun da marubuta sukan yi amfani da su wajen rubuta qagaggun labarai na Hausa. Takarda Wadda ya Gabatar don Sanin Makamar Aiki ta Qungiyar Marubuta ta Nijeriya (ANA) Xakin Taro na Murtala Ramat Muhammad, Kano.

Odell, L. (2007). *Elements of language.* New York: Holt, Rinehart and Wiston.

Strong, W. (2005). *Writer's choice grammer and composition*. United State of America: Glencoe.

Thomas, R. (2006). *Literature, structure, sound, and sense.* Canada: Michael Rosenberg.

Umaru, J.T. (1955). *Jiki magayi.* Zaria: NNPC.

Waziri, B.Y. (2012). "Dabarun bayar da labari a littafin ba a yi min adalci ba na (1) da na (2). Kundin Digiri na Biyu. Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Yahaya, I.Y. (1988). *Hausa a rubuce: Tarihin rubuce-rubuce cikin Hausa*. Zaria: NNPC.

Yakasai, A.G. (2007). "Nazari da Sharhi A Kan Littafin Tauraruwar Hamada na Sa'idu Ahmad daura". Kundin Digiri na Xaya. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

# RATAYE

DEPARTMENT OF NIGERIAN LANGUAGES

*(Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya)*

**VICE- CHANCELLOR**
Professor Muhammad Y. Bello
B.Sc, M.Sc(BUK) Ph.D.(Arkansas)
**Head of Department:**
**Dr. Aliyu Mu'azu**
**B.A, M.A, Ph.D (BUK)**


**Faculty of Arts and Islamic Studies**
**Bayero University,**
**PMB 3011, Kano-Nigeria**
**+234(80)23183152**
**Email: aliyum2006@yahoo.com**


15[th] May, 2017

The Head,
Department of African and Nigerian Languages,
Ahmadu Bello University,
Zaria.

Sir,

**<u>Introduction Letter In Respect of Hussaini Isah Muhammad SPS/15/MHA/00001 and 2 others</u>**

I write to introduce to you the above named persons who are our **M.A.** students in Hausa.

Kindly give them all the necessary assistance they may require to enable them pursues their research.

Thank you for your usual cooperation.

Yours faithfully,

Dept. of Nigerian Languages
BAYERO UNIVERSITY,
KANO.
**Aliyu Ibrahim**
For: Head of Department.

Department of African Languages & Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria
Date 9/6/17
Sign